[8/9, 4:06 PM] OPEN EYES MULTIMEDIA: *HABEEYTAH*
*_DUBAI PART 2_*

*FAUZIYYA TASI'U UMAR*
*UMMUH HAIRAN*

_FOR HAPPY SALLAH_

_Please ki biya kafin ki karanta nidai bazanyi Allah ya isaba Amma ban yafeba, da masu fitarmin da masu karantawa basu biya ba kuda Allah_

*1*

Gaban Habeey ne yayi wata muguwar faduwa ta zuba lumsassun idanunta akansa yayi saurin qasa da kansa tare da cewa “kibar wannan mgnr Granny don Allah muje ki bawa Habeeytah da babyna guri su huta tukunna komai dan nutsuwa ne"
Ajiyar zuciya kadai Habeey ta iya saukewa ta fara daga qafarta tana mayarwa inda Granny ta cire tata har suka shiga cikin parlourn ta rinqa bin parlour da kallo kamar bana tsohuwa ba, zaunar da ita tayi saman kujera ta zauna kusa da ita shima ya shigo ya zauna a gefen Granny.

Kallonsa tayi tace “ba yau zaka koma bane?" Agogo ya kallah yace “kalla agogo tsohuwa dare yayi bazan iya tafiya ba zan kwana zuwa safe saina wuce" murmushi tayi masa tare da cewa to bani da gurin kwananka a gidannan kaje BQ ka kwana in katashi da safe ma basai ka shigo ba ka wucce gdanku bana buqatar ciwon kai"
Hamma yayi yace “Granny inajin yunwa fah" qwalawa yar aikinta Kira tayi tace “ki kawowa mawa wannan ja'irin yaron abinci" shidai bai kulata ba saima zubawa Have ido da yayi duk jikinta a sanyaye yake ya sauke ajiyar zuciya ya miqe yace “Hajiya a kawomin abinci dakina ciwo yakeyi zan kwanta"

Bin bayansa Hajiya Dije tayi da kallo ta lura yau bayajin walwala, qwafa tayi ta miqe ta shiga

kitchen din ta zubowa Habeey tuwon ta dawo ta ajiye mata a gabanta ta riqo hannunta tace “sauko kici abinci kije ki kwanta ki huta" qasa tayi da kanta tace “inajin kamar na qoshi Hajiya" a zahiri bawai qoshin bane kadai zuciyarta Babu wani dadine da abinci zai samu guri a cikinta.
Dabi'ar Granny ita ba me qididdaga bace hakan yasa tace “badai kyau zana da yunwa kuma damuwa ba mafita bace saima qarin shiga matsala yanzu tashi muje kiyi wanka saiki kwanta" kamae me jiran umarni ta yunqura ta miqe Granny tanayi Mata sannu kadai taji wasu hawaye sun zubo mata, haka Granny ta shige ciki har dakin ta bude bandakin tace “kiyi wanka da ruwan dumi gajiyarki zata ware saiki kwanta"

Fita Granny tayi tabarta ita kuma ta fada bathroom ta sakarwa kanta tare da lumshe  tana shafa cikinta ta jima tanayin wankan tanajin sanyi cikin ranta bawai na gushewar damuwa ba saidai na ruwan da yake ratsata.
Dauro towel tayi ta fito ta tsaya gaban mirrow ta shafe jikinta da mayukanta masu qamshi taja Undersiket dinta har saman qirjinta babu pant bare bra ta haye gadon ta kwanta bacci me dadi ya dauketa.
Cikin dare taji an kwanta a kusa da ita  ta bude idonta a tsorace, ya sauke ajiyar zuciya tare da zura hannunsa cikin siket dinta yace “wlh na kasa bacci Habeeytah sha'awarki ta kumburamin burata bazan taba samun nutsuwa ba idan ba cinki nayi ba"

Tureshi tayi da sauri zata tashi yayi saurin hadata da katifar yace “dagani saike a qasa Granny tana sama tayi bacci, ki barni na huta Habeeytah damuwa tayimin yawa na rasa da wacce zanji bazan iyaba Habeeytah bazan iya auren wata bakeba ke kadai nakeso..."
Rufe masa baki tayi tace cikin kuka “bazan tabajin haushinka ba Taheer idan kayi aure zanmafi farin ciki da hakan dama nasan hakan zata faru na shirya zuwan wannan lkcn nifa Taheer kadai tsanarka nakeji a zuciyata narasa ya zanyi na sabawa kaina da sonk..."
Daga Mata hannu yayi yace “karki damu da sai kinji kina qaunata Habeeytah ni nasani kuma na yarda kinasona lkc ne baiyi ba da Zaki gane hakan nasan dai zamuyi aure duk tsanani duk wuya nine mijinki"

Rufeta yayi da qirjinsa ya fara sarrafata ta girgiza masa kai tana kuka tace “nayiwa Addah alqawari bazan qara zina ba Taheer kada ka takuramin nayit....." Yatsansa ya dora a bakinta ya dago cikin tsittsinkewar murya yace “wac...ce gudunmawa tabawa rayuwarki da zakiyi Mata alqawarin kasheni meye yasa kika sabarmin da ci daga jikinki bayan kinsan Zaki gujeni

Habeeytah wlh Allah ni nafi kowa sonki da son ganin rayuwarki ta inganta amma ya zanyi da kaina ni jarababbe ne akanki bazan iya hqra dake ba a halin inasonki kuma ina ganinki...."
Wawuro bakinta yayi ya hade da nasa jikinsa yana mazari ya hade dukkannin qarfinsa da Allah ya hore masa ya danne ta ya rinqa kissing dinta ta ko ina itakam yau batajin sha'awarsa wani haushinsa ma takeji idan ta tuna wai iyayensa aure zasuyi masa bayan ya gama lalata Mata rayuwa sai taji wani irin malolon baqin ciki ya tokareta a qirjinta hakanan bataso tanaqi tana tureshi ya budeta ya fara lasar gindinta jikinsa yana wata jijjiga.

Murza nononta yakeyi yana lashe ruwan gabanta yana budata yana lasheta ta shammaceshi ta miqe yayi wata uwar direwa ya cafketa ya cillata saman gadon ya janyo qafafunta ya buda yaci gaba da sarrafata.
Dukansa takeyi ta ko ina hardai yayi nasarar budata ya fara danna joystick dinsa a gabanta yana nishi yana kiran sunanta, saida ya gama daidaita zaman dick dinsa sannan ya kwanto ya sake cafkar nononta ya fara cinta da wani salo da bata tabajin irinsa ba dadinsa yana ratsata amma taqi nuna masa.
A rayuwarsa ya tsani wannan abinda takeyi masa yayita zura mata wutsiya amma taqi nuba masa jin dadinta hakanne yasashi farayi mata cin da yasan dole saita magantu, aikuwa kafin kace meye wannan ta fara ihun dadi tana kuka tanayi masa magiya shikuma yana ihun dadi zai sheqeshi ya bata lkc yana cinta kamar bazai daina ba sannan yayi release ya fadi gefe yana mayar da numfashi yana lasar lebe.
Janyewa tayi daga jikinsa a hankali ta miqe tana dafe cikinta saboda wani masifaffen ciwo da yakeyi Mata ta nufi bathroom ta tsugunna ta dafe bathtub tana jijjiga kanta tana hawaye tare da wani kuka me ciwo tanajin bayanta kamar zai rabe biyu.
Azabar ciwon qara gaba takeyi batasan sanda ta saki wata kidimammiyar qara ba data sanya Taheer dirowa daga gadon da gudu ya shiga bathroom din yagatan kwance riqe da ciki tanata juyi a qasa.......

_FOR HAPPY SALLAH_

*UMMUH HAIRAN*
[8/9, 4:06 PM] OPEN EYES MULTIMEDIA: *HABEEYTAH*
*_DUBAI PART 2_*

*FAUZIYYA TASI'U UMAR*
*UMMUH HAIRAN*

_Please ki biya kafin ki karanta nidai bazanyi Allah ya isaba Amma ban yafeba, da masu fitarmin da masu karantawa basu biya ba kuda Allah_

*2*

Da sauri ya fita ya dauki boxes dinsa ya sanya ya koma ya sake kamota jikinsa yace “Hab...beey meye inane garin yayane ciwi naji miki" daga kanta tayi idanunta a lumshe yana zubar hawaye tana qara riqe cikinta ya dagata da azama ya fita da ita ya kwantar ta ya fice. Sama ya haura da sauri ya shiga knowking qofar da zata kaishi dakin baccin Granny, bugun taji bana hankali ba ta miqe da sauri ta fito ta bude taganshi tsaye tace “Ify?" Hannunta ya kama yace “bansan meye matsalar ba amma Habeey batada Ify sai riqe cikinta takeyi"

Binsa tayi suka nufi qasan suka shiga dakin suka tarar da ita a qasa cikin ysnayin azabar ciwo, da sauri suks matsa suka kalli juna yace Granny ko asibiti zamu kaita ne tanajin jiki fah" tsugunnawa Granny tayi tace “cikinta wata nawa ne?" Yanakai hannunsa zai dauki Habeey din yace.
“Wata bakwai..." Bai iya qarasawa ba saboda yanda yaji ta fara jijjiga a guje sukayi waje cikin tashin hankali suka sanyata a mota Granny tayiwa security mgn suka rufa musu baya suka nufi wani asibitin kudi dake cikin garin azare.
Suna zuwa suka dauketa suka nufi wani daki da ita suka fara kulawa da ita, sunsha wahala ta sosai kafin susa mata ruwan naquda saboda ganin ana Shirin yin biyu babu, da taimakon Indurcing din da sukayi mata da Kuma jajircewarsu suka ciro mata kyakkyawar qatuwar yarta me masifar kama da Taheer suka duqufa wajen ceto tata rayuwar.

Fita sukayi da jaririyar da nufin kaita dakin da zaake kula da ita Taheer dake zaune ya hade kai da gwiwa sai bugawa zuciyarsa takeyi ya dago da sauri ya nufosu Dr yayi masa murmushi

yace.
“Anyi nasarar ciro maka baby girl dinka tana cikin qoshin Ify saidai batakai lkcn haihuwa ba zaa kaita dakin kulawa ita kuma uwar tana cikin halin commer sakamakon hatsarin jijjiga data samu saidai ku tayamu da addu'a Allah ya dawo da ita cikin hayyacinta nan da qarfe biyun rana idan ba hakaba komai zai iya faruwa.
Ba Taheer ba hatta Granny saida cikinta ya kada wasu hawaye masu zafi suka zubo masa yace “Dr kada kuyi sakaci don Allah Tanada muhimmanci a rayuwata" dafashi yayi yace “insha Allahu komai zaizo da sauqi"

Matsawa yayi ya leqa fuskar yar tasa kyakkyawa da ita ya sauke ajiyar zuciya tare da miqa hannu ya karbeta ya zauna ya zuba mata idanu yanajin wani tausayin kansa da Habeey da Kuma yar tasu da yake fatan ta zame masa raba gardama ko kamar da yarinyar takeyi da Mom dinsa ya isa yasa zuciyar Mom tayi sanyi tabarsa ya auri Habeey dinsa.
Da wadannan tunane tunanen Granny ta matso ta kalli yarinyar tace “masha Allah Lele kamar kumbo kamar katanta ga tukuicin sabawa ubangiji nan ka samu sai kayita kallonta a matsayin yar zina..." Ji yayi qirjinsa ya buga yace “Granny don Allah kada ki qara fadamin haka nifa banson a dangantamin yata da laifin dana aikata ba ita tayiba"

Karbarta likitan yayi yace “muna buqatar jini uwar ta zubar da jini sosai zaa daura mata" miqewa yayi yace “zaa iya diba a jikina jininmu iri dayane"
Dakin da zaikai babyn ya shiga yayi Mata abinda ya dace sannan ya dawo suka nufi Lab suka debi jinin nasa duk da haka saida aka nemi qarin leda daya aka siya aka sanya mata.
Ranar a asibitin dukkansu suka kwana saida asuba Granny tace yaje ya nemo musu kayan amfani ya kawo musu, aikuwa taga hauka kaya kamar zasu bude shago ya kawo musu lkcn da aka fito da kayan fada Granny ta farayi tace maza ya rage yakai gda aiba dawwama zasuyi a asibitin ba.

Zama ya nemi  guri yayi yace “saidai ki rabar bazasu koma ba gdanma akwai ukun wadannan" bata qara cewa komai ba ta koma ta zauna tare da kiran wayar governor Waziri.
Tun jiya yake Kiran wayar Taheer yaqi dagawa ganin kiran mahaifiyar tasa yasashi dagawa da sauri zuciyarsa na bugawa saboda tunanin ko meyene dalilin Kiran da safe haka.
Sallama yayi mata tace “Ify Lau Wazir ka fadawa Safinah Habeebah budurwar Taheer ta haifi ya mace me kama da ita yanzu haka muna tare anan azare..." Wata firgita Alh Waziri yayi yace “what Inna haihuwa kuma? Wai dama da gaske yaron nan yakeyi ciki yayiwa yarinyar nan haba Inna ya zakiyimin haka don Allah ya zaayi ki daurewa yaron nan gindi yaci gaba da iskancinsa kina gani fah tun jiya da mukayi masa mgnr sa ranar aurenss da Saudat ya fice bai sake

waiwayenmu ba kiran duniya yaqi dagawa qarshe ma yasa uwarsa a blacklist haba Hajiya wannan ai zubar mana da qimane da mutunci, kamarni ace....."

Katseshi tayi da cewa “koma mene aikin gama ya gama Taheer yayiwa budurwarsa ciki ya kawomin ita gata a hannuna kuma dama ai tarbiyyarku ce hakan abinda yaranku sukeso shi zakuyi musu saboda haka shima ku barshi da abinda yakeso sannan qaddarar yaya tanakan kowa itama ba haks iyayenta sukaso ba rubutun tawadar ubangijine sai ta hadu dashi sunyi wannan abin kunyar"
Kashe wayarta tayi ta karbi babyn a hannun Taheer dake shigowa ya zauna yana kallonta tana goge mata jikinta tana shafa Mata zaitun tare da tofa Mata addu'o'i a jikinta tasa mata Pampers ta sanya Mata kayan sanyi tace “kayi mata huduba kuwa?" Girgiza kai yayi ta Kuma cewa “saboda me?" Bude runannun idanunsa yayi yace “na rasa sunan da zansa Mata  Granny” murmushi tayi tace “kasa Mata Safinatul Najah" da sauri ya dago yace “sunan Mom?" Daga masa kai tayi tace “eh akwai ma'ana a cikin hakan"

Ajiyar zuciya yayi ya karbeta yayi mata hudubar yanajin qaunar yarinyar tana mamaye duk wani gurbi da qaunar uwarta ta rage a zuciyarsa dagowa yayi yace “tun ranar da na fara bata rayuwar Habeeytah Allah ya jarabceni da qaunarta har inajin kamar mutuwa zanyi idan ban aureta ba Granny nasani Habeey batasona saboda tana kallona kallon mafi munin qaddararta don Allah ki shigemin gaba muyi aure da ita badon kaina ba saidon maslahar rayuwarmu dukkanmu da ta Safnah"
Mamakine da tausayinsa ya cika zuciyar Granny ta dafashi ya dago kansa kawai sai taga hawaye yana shatata a idonsa tace “subhanallahi Lele meye kuma abin kukan a cikin wannan lamarin mutum ko yaqi Allah ai bazaice maka aa ba saidai babbar matsalar shine daidatawar yarinyar nan da mahaifanta"
Share hawayen yayi ya miqe ya matsa gaban gadon da take yace “ban damu da kowa yaso tarayyata da Habeey ba burina kawai itan ta amince dani ta daina yimin kallon da takeyi min Granny inason Habeeytah nini kadai na dace da zama mijinta saboda nine silar kowacce irin lalacewa tata"..........
# *UMMUH HAIRAN*
[8/9, 4:07 PM] OPEN EYES MULTIMEDIA: *HABEEYTAH*
*_DUBAI PART 2_*

*FAUZIYYA TASI'U UMAR*
*UMMUH HAIRAN*

_Please ki biya kafin ki karanta nidai bazanyi Allah ya isaba Amma ban yafeba, da masu fitarmin da masu karantawa basu biya ba kuda Allah_

*3*

Kansa ya dora a qirjinta yaji yanda numfashinta yake sauka so slow ya shafa fuskarta ya sauke murmushi ya kwantar da babyn a kusa da ita ya fice, Granny miqewa tayi taje ta tsaya kan Habeey ta zuba Mata ido gabanta na tsananta faduwa har baccinta irin na Sahabinta ne hatta fatarta itadai wannan kama tana bata mamaki tabbas da ace sahabi yana qasar nan da zatace wannan yarinyar akwai wani Abu da ya hadasu.
Komawa tayi ta zauna tanaci gaba da kallon fuskar Habeey a fili tace shekara goma sha tara kenan da sahabi ya koma England da zama baitaba zuwa ba Koda ziyara, share hawayenta tayi tace “idan na mutu qila zaizo"

A haka Dad yazo ya sameta a firgice ya shigo ta miqe da sauri ya daidaita tsaiwarshi yace “haba Inna meye hak....." Maganarce ta maqale a bakinsa Ikcn daya sauke idanunsa akan fuskar Habeey maimakon ya qarasa abinda yake Shirin fada sai ya qarasa da fadin “Sas...sahabi"
Kallonsa Granny tayi da sauri tace kaima ka gani ko Aliyu na dauka ni kadaice nake ganin kamar nayi tunanin qulafuci na dason ganinsa ne yasa nake ganin wannan yarinyar tanamin kama dashi"
Zama yayi dabar a qasa yace “tunda nake bantaba ganin abinda ya tsinkamin laka irin wannan halittar ba Inna a Ina Taheer ya samo wannan yarinyar?" Share kuncinta tayi tace “bansaba Aliyu nidai inajin tsoron wani Abu"

Girgiza kai yayi yace “karki kawo wannan a ranki babu haka a files din rayuwar Sahabi kawai dai kamace Kuma kinsan ita halittar ubangiji aya ce nasan shima Taheer bai taba kula ba Koda yake baisan baffansa sahabi ba sai awaya"
Miqa hannu yayi ya dauki yarinya dake ta baccinta ya zauna yana qare Mata kallo a hankali ya hadiyi yawu me ciwo ya dago idanunsa da suka kada sukayi jawur ya zubasu akan fuskar Taheer da suke shigowa da likita, yayi saurin kawar dakai daga kallon Dad yana cewa likitan “kazo ka dubata idan bazaku iyaba na fita da ita waje kawai"

Juyawa Dad yayi yana kallon sarautar Allah bai iya cewa dashi komai ba har saida likitan ya gama abinda zaiyi ya fita shima ya juya zai fita sannan yayi gyaran murya tare da kiran sunansa.
Tsayawa yayi ya juyo a sanyaye hawayen da yaketa kokawar tsayarwa suka zubo masa sosai yake tausayin mahaifinsa saboda yasan wannan abinda yayi kamar sanya fetur ne ya qasta ashana saman martabar Governor Waziri, yafitosa yayi yazo ya zauna yace “inayi maka murnar samun qaruwa da kayi Taheer Allah ya raya maka ya bamu ikon tarbiyantar da Safnah bisa sunnah"
Dagowa yayi idanunsa na digar hawaye yace “Dad..."daga masa hannu yayi yace “ya zamuyi dakai Taheer tunda mun haifeka hakamma na godewa Allah ni kuma dakai da Dan'uwanka ya jarrabeni Taheer Mahfuz kun zamemin jarabawa a rayuwata"

Girgiza kai yakeyi sosai yana kuka me cike da nadama yace “wlh Dad ko yanzu idan baku amincemin na auri Habeey ba bazan iya riqe kaina daga gareta ba saboda zuciyata ita kadai takeso"
Murmushin takaici yayi yace “zaka aureta Taheer gara nabaka abinda kakeso kafin ka jamin abinda yafi wann...."
“Wlh tallahi bazai aureta ba Aliyu" cewar Mom da take shigowa kenan, tsayawa tayi a gabansu tace “bazai taba yuwuwa ka cakudamin zuri'a da shegu ba sannan ka canzawa shegiyar yarka suna baka isa ka shegantamin suna ba...." Miqewa yayi yace “don Allah ya isa Mom Habeeytah batason hayaniya kada ki tasheta..." Wani daukakken ta sauke masa wanda yaga tartsatsin wuta a idanunsa ya zuba mata ido tare da sauke numfashi
# *UMMUH HAIRAN*
[8/9, 4:07 PM] OPEN EYES MULTIMEDIA: *HABEEYTAH*
*_DUBAI PART 2_*

*FAUZIYYA TASI'U UMAR*
*UMMUH HAIRAN*

_Please ki biya kafin ki karanta nidai bazanyi Allah ya isaba Amma ban yafeba, da masu fitarmin da masu karantawa basu biya ba kuda Allah_

*4*

Ashar ta danna masa ta matsa ta fincike robar jinin dake maqale a hannun Habeey ta cafki wuyanta tana jijjigata tana fadin “wlh baki isa ki zama surukata ba tsinanniya matsiyataciya yar tasha karuw..." Wani kira dayakeyi Mata tare da finciketa daga jikin Habeey dinne ya dawo da ita hayyacinta ta saki wuyan habeey da sauri taja baya.
Tana kallon yanda take fitar da numfashi a wahalce ga wata kumfa da take fitarwa a bakinta tayi saurin juyawa zata fice governor Waziri ya kira sunanta tare da cewa “kafin ki fita kisan da saninki indai yar mutane fa mutu sanadin taaddancinki wlh sai kinyi zaman jarun"

Wata ajiyar numfashi Habeey tayi komai nata ya daina motsawa Taheer ya dira gabanta ta dagota yana danna qirjinta yana Kiran sunanta Dad ya miqe da sauri ya fita yaje ya taho da likitan itakuwa Mom tayi wuqi² cikin tsoro da tashin hankali Granny kuwa mamakin lamarin Mom ne ya hanata cewa komai sai dauke Safnah da tayi tasata a sabon gadon da ubanta ya siyo mata.
Rufuwa likitocin sukayi akan Habeey harda Taheer sun bata sama da awanni uku sannan suka samu numfashin ya daidaita suka fito zuwa lkcn Mom ta sace jikinta tabar asibitin ta wucce gidan yayarta tana kuka take zayyane mata komai har auren Saudat yar qanin Dad Sahabi data nema masa tasa Saudat ta dawo daga England kawai saboda ta hadata da Taheer amma abin yana neman  gagara.

Yanda take kuka yasa Hajiya Ummah yayarta dariya tace “kece uwa kece kike da wuqa kike da nama fah yanzu dai shawara daya itace tunda ya kafe saiya auri yarinyar nan ki qyaleshi ya aureta din kodan rufuwar asirinku game da wannan yar kafin fatiha din ayi auren cikin sirri ta tare ta yanda babu Wanda zaisan ba aure aka haifeta"
Girgiza kai tayi tace “aikin gama ya riga ya gama Ummah sirrin dan siyasa baya buya ni kaina baa gurin Taheer naji haihuwar ba kirana akayi da baquwar number aka fadamin karuwar dana ta haihu a asibiti kaza har lambar dakin aka turomin"

Shiru sukayi na wani dogon lkc sannan Ummah ta magantu da cewa “shawara ta biyu kije ki hada baki da likitan ayiwa jaririyar allurar guba ta mutu kowa ya huta..." Da sauri Mom ta kalli Ummah tace “kuma nayi kisa Ummah aa bazan iya ba nikam inajin tsoro na lura daga Granny har Dad hankalinsu yana kan wannan jaririyar"
Murmushin takaici Ummah tayi tace “shikenan kije zanyi tunanin mafita kafin a sallamesu daga

asibiti cikin wata biyun da kukasa na bikinsa da Saudat dole ne a mantar dashi tunanin wannan karuwar yarinyar idan ba hakaba tabbas da matsala don zama ku iya daura masa auren ya saki matar" miqewa Mom tayi tace “dakuwa na tsine masa ya qarasa lalacewa"

Da haka ta fice a gdan driventa yajata suka fice suka nufi government house suna tsayawa ta fito ta shiga gdan bangaren yammatan nata ta shiga ta tarar dasu sun rufu akan Saudat sunata rarrashinta itakuma sai kuka takeyi, salati Mom tayi ta shiga cikin dakin tana tambayarsu menene.
Kuka bai bari Saudat tayi bayani ba sai shassheqa da takeyi Bushirah tabe baki tayi ta shige bathroom Kubrah ta dago tace “Yaya Taheer ne ya dawo ya shiga dakinsa yana neman wani abu kawai ita kuma sai tabisa dakin munyi qoqarin hanata taqi hanuwa, bamusan me tace masa ba kawai sai gani mukayi ya fito da ita a hannunsa ya jefar da ita a parlour yana jibgarta kamar Allah ya aikosa yana gama dukanta ya fice ya hau motarsa yabar gdan itakuma munyi munyi da ita ta fada mana me tace masa taqi"

Zama Mom tayi zuciyarta na tafasa tace “ke me kikace masa da yaja miki wannan dukan sa'ar haka?" Cikin shassheqar kuka tace “wai...wai don na shiga ya fito daga wanka shine na matsi mai zan shafa masa ya juyo ya dakamin tsawa wai na fice masa daga part shi...shine nace karuwa ma ta samu Ikcnsa balleni da zanzama matar sunnah shine ya juyo yacemin wai karna qara cewa da uwar yarsa karuwa domin tabashi abinda a duniya babu wanda ya amince ya bashi sai itadin kuma Koda zaa bashi to bayan wadda tabashi zasu biyo, nikuma sai nace ai ko a shari'a shege bashida gado saboda haka matsayin dan halak yana sama qololuwa dana dan zina, wlh Mom ban qaraba ban rageba kawai naji ya shaqeni ya hadani da bango ya gwaramin kaina da gini ni bansan ya akayi ba kawai saiji nayi ya zubar dani a parlour yasa belt ya rinqa dukana kamar jaka daqyar su Solomon suka qwaceni...."

Ta qarashe mgnr cikin gunjin kuka ta zame bayanta Mom tayi saurin rintse idonta saboda yanda ya farfasa Mata jiki da belt tace “yanzu Mom haka zan rayu da Yaya Taheer babu tausayi babu soyayya ace karuwa ma tafika matsayi a gurin mijinka, gsky Mom da sake duk da inason Taheer Allah ya jarrabi zuciyata da qaunarsa tun bangansa a zahiri ba Mom zan iya jure kowanne wulaqanci a gurinsa indai zai rayu dani matsayin matarsa saboda nasan yanda ciwon so yake nasan abinda yakeji Mom amma bazan dauki duka akan karuwa ba Mom waini meye Habeeytan nan da yake yawan ambata take dashi dani bani dashi? Meye tafini don Allah ki fadamin meye aibina da Yaya Taheer yaqi naam da soyayyata duk da kasancewata yar uwarsa ta jini wacce na yarda da naqasunsa da komai na aminta zan rayu dashi a haka"

Shafa kanta Mom tayi ta share mata hawayenta tace “na rasa meye yasa Taheer ya zama me taurin kai akan yarinyar nan wlh a baya duk abinda na nuna masa bana raayinsa duk son da yakewa abinnan ya hqr dashi amma nakasa juya zuciyarsa akan yarinyar nan wai harni Taheer yake kallo yacemin indai ban janye auresa dake ba nabarsa ya auri Habeey ba to shakka babu zakiyi nadamar zuwanki duniya kuma zina yanzu yafara saboda zuciyar Habeey a hannunsa take duk yanda yayi da ita haka takebi, Saudat zanji tsananin kunyar Sahabi da Zahrah qanwata idan har nakasa tanqwara zuciyar Taheer ya aureki bari kiji wani Abu" kunnenta ta kama ta rada Mata wata mgn sukayi dariya tare da rungumeta tace “shiyasa nake sonki Mom har mafarkin first night dina a gidan Yaya Taheer nakeyi yauma saida nayi mafarki ganinan a kwance a qirjinsa yanata shafa sumata"

Rufe mata baki tayi tana dariya tace “saudat bakida dama wai yaushe Abbanki zaizo 9ja ne?" Lumshe idonta tayi tace “yacemin tunda ya rasa “Matarsa ta fari Hajar Ikcn da cikinsa watanni uku a jikinta ya fara wannan ciwon zuciyar yakejin idan an ambaci 9ja gabansa na faduwa yacemin kullum mafarkinsa shine yazo 9ja amma gani yake kamar idan ya dawo abinda ya faru shekaru ashirin da daya baya shine zai qara faruwa"
Girgiza kai Mom tayi tace “har yanzu Sahabi yana mafarkin ganin wannan Dan nasa ko yarsa don ko jiya da mukayi waya da Mamanki take cemin wai yanzu firgita yakeyi yana yawan Kiran sunan Hajar yana ambaton Ina dansa ko yarsa? Kuma fah bayan rabuwarsu ance nemanta akayi aka rasa wasu ma suna cewa ta mutu"
Share hawayen tausayin abbanta Saudat tayi tace “nima kullum Ina addu'ar indai dan uwana ko yar uwata tana raye tazo gareni ko yazo gareni Mom kadaici ya isheni Mom banida abokin kuka banida na dariya banida shaqiqin da zanyi hira dashi naji dadi nasan yanzu da dan'uwana ko yar'uwata tana kusa gareni da zata rinqa tausata da tayani addu'a akan wannan mugun son da nake yiwa Yaya Taheer shikuma baya sona dama tun Ina qarama Yaya Taheer ya tsaneni" ta qarashe maganar cikin kuka me narkar da zuciya.

_Gareku masoya garabasa gareku saboda murnar bikin babbar sallah daga yau 3/8/2020 zuwa_ _10/8/2020 na rage kudin da ake biya domin samun wannan_ _rikitaccen labari me cike da turka turka single Zaki biya 150 VIP 400 idan ta account ne._
_Account 0255526235 Fauziyya Tasi'u Umar GTB, saiki tura evidence_ _of payment ta wannan number 09013718241_
_Idan katine kuma Zaki biya 200 VIP 400 ta wannan number_ _09013718241 kada ki manta lambobin katin ake buqata ko hotonsa._

# *UMMUH HAIRAN*
[8/9, 4:07 PM] OPEN EYES MULTIMEDIA: *HABEEYTAH*
*_DUBAI PART 2_*

*FAUZIYYA TASI'U UMAR*
*UMMUH HAIRAN*

_Qarshen free page na Happy sallah_

_Please ki biya kafin ki karanta nidai bazanyi Allah ya isaba Amma ban yafeba, da masu fitarmin da masu karantawa basu biya ba kuda Allah_

*5*

Shafa kanta tayi tana tausarta saboda tasani iyayenta basason bacin ranta shiyasa take lallabata saboda a gudun abinda kaje yazo amma taci alwashin duk yanda Taheer zaiyi saidai ya mutu aure tsakaninsa da Saudat babu fashi.
Yini sukayi tanata rarrashinta hardai ta samu ta ware Bushirah da Kubrah suka fito cikin shigarsu ta alfarma suka tarar dasu a parlour Mom ta dubesu tace “Ina zakuje?" Cikin yauqi Kubrah tace “zamuje mugano yarmu ne kada Yaya yasamu a blacklist" wata uwar harara ta watsa musu tare da jan tsaki ita kuwa Saudat mutuwar zaune tayi saboda mamaki wai zasuje su gano yarsu yar zinar?

Bushirah ce ta dubi Saudat tace “dama kin tashi munje kya ragewa kanki damuwar son maso wani ko banza kyaganshi acan gurin gudaliyar yarsa da matarsa da yakejin amutu ko a rayu a kanta"
Wasu hawaye ne suka zubo mata ta miqe ta shige daki ta fada gado ta rushe da kuka ta fahimci a gidan daga Mom sai Dad sune suke sonta yaran gidan gabadaya yan partyn abinda Taheer keso ne hatta da Mahfuz da baya qasar da aka kirashi aka fada masa cewa yayi kema dai Mom shirme kikeyi kinsan dai blood bazai taba yi miki biyayya ba indai akan baben nan ne wlh Mom ni kaina don dai  blood ya rigani afkawa ne badon hakaba da tafi haka zaayi, Mom ki share kawai irin wannan auren fah dadine dashi tasanshi yasanta awonsu daidai ne Zaki wani zo ki hadashi da wata qyailar yarinya...."

Kalaman na dawowa Saudat tanajin bugun zuciyarta na qaruwa ta miqe zumbur ta fita ta tarar dasu suna shirin tashin mota ta qarasa da sauri ta bude ta shiga suka kalleta sukayi dariya Kubrah tace “iska tana wahalar dame kayan kara nifa banga abinda zaisa na rinqa bata lkc na akan namijin da baya sona ba musamman Yaya Taheer me masifar tsaurin raayi kinaji fah a gabanki Jabir yake fadawa Mom ita kanta Habeeytah bata tsira daga wulaqancinsa ba idan ya tashi itama da yake iqirarin yanaso kenan balle ke yar karere"
Itadai Shiru tayi batace qala ba har suka dauki hanya suka fara tafiya sunata hirar samarinsu Saudat dai bata cewa komai sai tsiyayyar hawaye.

Sai magrib suka isa suna zuwa sukayi parking suka fito daidai lkcn yana fitowa da waya a kare a kunnensa yana cewa “wlh blood bakaga babyn ba kamar kai itama da Mom take kama nayi Mata huduba da Safeenatul Najah....."
Katse maganar yayi lkcn da sukayi karo da Saudat yayi baya da sauri tare da tsartar da yawu yace “ke wacce irin banza ce bakya ganine" cikin rawar jiki tace “ban...ban kula ba Yaya Taheer kayi hqr" tsaki yayi ya matsa gurin yan uwansa suka rungume juna dama gaisuwarsu kenan yace “ashe zakuzo na dauka Mom bazata barku ba" dariya Bushirah tayi tace “ai dole abu namu maganin a kwabemu"

Dariya sukayi dukkansu banda Saudat data zubawa sarautar Allah ido ya kama hannunsu suka shiga dakin Granny tana sallah itakuwa Habeey tana kwance kamar gawa saboda shaqar da Mom tayi Mata ta mayar da ciwonta farko, ya saki hannunsu ya matsa ya sanya hannunsa ya tattare Mata gashinta daya rufe Mata fuskarta yayi kissing lips dinta yace “a kowanne hali kyaune dake Habeeytah"
Gyaran muryar Granny yasashi saurin janyewa kunya kamar ya nutse ya juyo tare da sosa kansa ta sakar masa ranqwashi tace “kaikam kwai fitinannen namiji a jinyacen ma bazaka qyale yar mutane ba anya kuwa Taheer ba Mata hudu zan aura maka ba?"

Murmushi yayi yace “bazasu mayemin gurbin Habeeytah ba ita kadai gayyace Granny a duk matan duniya babu wacce zata iya dani sama da Habeeytah" wani mashine ya caki zuciyar Saudat tayi saurin juyawa zata fita Kubrah ta riqo hannunta tace “bakiga yar taki ba don nasan

a hannunki qila zata rayu" sake hadiye wata kibiyar baqin ciki tayi ta caki qahon zuciyarta ta nemi guri dabar ta zauna.
Shikam yama manta da an halicceta a gurin surutu kawai yakeyi yana fasaltawa Granny irin son da yakeyiwa Habbatullah tare da zubawa Safnah ido yana murmushi yace “wlh Granny ji nakeyi kamar na hadiye my daughter saboda nakasa fasalta irin son da nakeyi mata nifa yanzu ko ke kikace bakison yata Allah idan muka rabu har abada bare wani banza da rayuwata batayi kama da tasaba dan karere"

Sarai duk wanda yake gurin ya fahimci da wadda yake amma shi har cikin ransa bada itan yakeba, Bushirah ce ta karbi Safnah ta zuba Mata ido tace “wow! Yaya wannan babyn kamar jinin larabawa Masha Allah amma Yaya kamar ba bakwaini ba"
Granny ce  “nima da aka haifeta nace ba bakwaini bace saida likitan ya aunata yace kawai dai me girmance amma watanta bakwai da kwana daya a cikin mahaifa yanzu ma ance a daina jagwalgwalata amma wannan dan rawar kan yaqi barinta ta huta" murmushi yayi yace “aini dama komai zanyi ban iyaba indai a gurinki ne tsohuwa dake"
A kasalance Saudat ta taso ta leqa fuskar yarinyar ta zuba mata ido tanajin faduwar gabanta na tsananta a ranta tana raya dama itace ta haifa masa ita qila da soyayyar yarinyar zatasa yasota itama.

Miqo hannu tayi zata karbeta yayi saurin dauke abarsa yaje ya kwantar da ita a kusa da uwarta sai yanzu Saudat ta samu damar kallon Have dake kwance matsayin gawa tayi saurin matsawa gabanta tana furta “lahaula wala quwwata illah billahil aliyul'azeem" hannunta takai zata taba fuskar Habeey yayi saurin riqe hannunta cikin tsawa yace.
“Idan kika kuskura kika tabamin mata wani abu ya sameta wlh sai nayi shari'a dake gabadayanki na tsaneki Saudat...."
Rufe masa baki tayi jikinta na rawa tace “nikuma inasonka a haka Yaya kuma saina aureka Koda kuwa zaka kasheni don qiyayya, Taheer ba takai nakeyi ba yanzu na gama dakai domin ko kanaso ko bakaso saika aureni dole"..........

_Gareku masoya garabasa gareku saboda murnar bikin babbar sallah daga yau 3/8/2020 zuwa_ _10/8/2020 na rage kudin da ake biya domin samun wannan_ _rikitaccen labari me cike da turka turka single Zaki biya 150 VIP 400 idan ta account ne._
_Account 0255526235 Fauziyya Tasi'u Umar GTB, saiki tura evidence_ _of payment ta wannan number 09013718241_
_Idan katine kuma Zaki biya 200 VIP 400  ta wannan number_ _09013718241 kada ki manta lambobin katin ake buqata ko hotonsa._

# *UMMUH HAIRAN*
[8/9, 4:07 PM] OPEN EYES MULTIMEDIA: *HABEEYTAH*
*_DUBAI PART 2_*

*FAUZIYYA TASI'U UMAR*
*UMMUH HAIRAN*

*6*

Tsayawa tayi sake da baki yana kallon ikon lillahi wai saita aurets dole ko a Ina aka taba yiwa namiji auren dole? Murmushin tausayinta yayi shi gabadaya ya gama raina hankalinta hakanan yakejin amai yana taso masa idan ya kalleta.
Juyawa yayi ya fice daidai lkcn wayarsa tayi qara ya daga da sauri tare da kasheta ya mayar aljihunsa kusan ko yaushe a tsakanin jiya da yau sai an kirashi da number qanin na habeey Ibrahim shikuma haushin abinda Addah tayiwa Habeey akan cikinsa yasa yaji ya tsani duk wani wanda ya rabeta basu da adalci dangin Habeey ko kadan basusan darajar dan Adam ba, basu da damu da itaba itace ta damu dasu take sadaukar da komai domin danginta.

Da wannan tunanin ya shiga mota yana Shirin tashinta qannen nasa suka fito Bushirah ta matso gabansa tace “sati biyar akasa aurenka da Saudat Yaya a halin da aka ciki Habeey da Safnah sunfi kowa buqatarka don Allah kada kayi sakacin da baiwarka Allan nan zata qara shigs gararin rayuwa Yaya Taheer jin Habeey nakeyi kamar yar uwata ta jini"
Riqe hannunta yayi yace “karki damu qanwata babu Wanda ya isa yayimin auren dole auren ma da wannan tsakuwar yarinyar haba suma su Dad wasa sukeyi wlh Idan suka suka matsa zan iya farke shegiya ta mutu kowa ya huta"

Yana gama fadin haka ya figi motar a guje ya nufi gidan Granny ya shiga bangarensa na gidan yayi wanka ya kwanta ya fara aikin sanar da abokansa cewa anyi masa haihuwa mamaki sukeyi sosai yaushe yayi aure da har matarsa ta haihu.
Shikam ko a jikinsa gani yakeyi ai shima aiki yayi ya samu abarsa sabida haka ya cancanci a tayasa murna, daya gama buge bugen wayar tasa sai ya budo hoton sahibar tasa da yar tasa ya rinqa kallo yana murmushi har bacci ya daukesa.
Cikin sati biyun da habeey tayi a asibiti abubuwa da dama sun faru ciki harda qarfafuwar mgnr

auren Taheer da Saudat tabbas Saudat tana cikin matsananciyar damuwa saboda Wanda takeyi dominsa din baisan tanayi ba tana kallon yanda Khamal da Sudess samarin su Kubrah suketa rawar qafar bikin amma banda nata angon dako kallon tsiya bata samu a gurinsa balle na arziqi.

Da taimakon Hajiya Ummah yayar Mom da Zahrah mahaifiyar Saudat aka shiga aka fita aka cusawa Taheer jin tsanar Habeey a ransa sunyi duk me yuwuwa su cusa masa qiyayyar Safnansa amma abin ya faskara saima kamar qara masa qaunar yarinyar da akeyi.
Cikin sati biyun jikinta ya fara kyau sosai ta fara sanin waye yake a kanta, farkon fari kullum a asibitin yake yini amma yanzu sai ya yini sur baizoba saidai ya kira a waya yaji ya babensa, wannan canji ya tashi hankalin Granny da Bushirah dake jinyar Habeey da farko sun dauka mgnr auren nasa ce tasashi a busy amma sai Bushirah ta lura shima auren ba wani murna yakeyi dashi ba kullum ka nemeshi zaka sameshi a garden ya hade kai da gwiwa yanata karatun wasiqar jaki"

Yau ta kama asabarce wadda tayi daidai da satin Habbatullah hudu a asibiti misalin qarfe biyu na rana ta fara motsa qafafunta tare dayin attishawa daga Kubrah har Bushirah da Granny dama Addah da ciwon yar tata yasata saukowa shima Bushirah ce tayi tattaki taje ta sanar da ita.
Dukkansu kanta sukayo ta muqar da hannunta tare da amsa kalmar shahadar da Addah take laqaba mata ta riqe qam tanayi tana girgiza kanta, fita Bushirah tayi da gudu ta fadawa likitan abinda yake faruwa daidai lkcn da likitan ya iso daidai lkcn Taheer suka shigo shida Saudat a zahirin gaskiya shi kansa baisan Saudat ta biyosa ba saboda kaca² suka rabu dutsi a hannun riga amma sai gashi sun shigo tare kafadarsu na gugan juna.

A lkcn ne Habbatullah ta fara bude idonta a hankali tana kallon kowa dake dakin da fuskar rashin sani har takai ga sauke idonta akan Addah ta zabura zara miqe likitan yayi saurin riqeta tare da cewa.
“Kibi a hankali Hajiya zaki tashi insha Allahu" a sanyaye da murya ta alamun jin jiki tace
“Ad...Addah ashe zakizo gurina ashe har yanzu kina sona Addah ina qannena Aysha da Fatima ina Taheer Addah ki kiramin shi don Allah" juyawa Kubrah da Bushirah dama kowa dake gurin sukayi inda yake tsaye yana danna wayarsa.
Wani mugun kallo Addah takeyi masa a cikin kwana ukun da tayi a asibitin yaune ta fara ganinsa taja ajiyar zuciya hakanan takejin tsanar Taheer a ranta kuma ta qudurce a ranta indai

yarta zataji mgnrta to zata rabata dashi rabuwa ta har abada.

Matsawa Bushirah tayi kusa dashi ta warcr wayar hannunsa tace “haba Yaya kanaji sai kiranka Habbatullah takeyi Amma ka wani basar...." Bata rufe bakinta ba ya sauke Mata wani gigitaccen mari ya sakeyin bal da ita yace.
“Wata banza dake Zaki qwacemin wayata saime to dan wannan banzar ballagazar ta kirani dama jira nakeyi ta warke Kuma alhmdllh ta warke banida haqqinta zata iya komawa inda ta fito Amma karki sake ki daukarmin yata inason abata Saudat zata riqemin ita, yawwa ladan haihuwar kyakkyawar baben nan da kikayimin na mallaka miki gidana dake layin gdan sarkin Bauchi ki duba wayarki nayi miki transfer ta million hamsin nasan ta isheki ki qarashe rayuwarki na bakisu a matsayin fansar budurcinki"

Yana fadin haka ya ajiye Mata want a saman cinyarta ya juya zai fita ta bude bakinta jikinta na rawa tace “na roqeka da girma da matsayin ubangijin daya sanya tausayi da jinqai tsakanin bayinsa kada ka juyamin baya Taheer karka manta kayimin alqawarin duk tsanani bazaka gujeni ba bazaka juyamin bayaba wlh na amince zan aureka Taheer kada ka wofintar dani Ikcn da nake tsananin buqatar jin qanka...."
Ta qarasa mgnr cikin sarqewar numfashi baiko qarasa jin abinda zata fadaba ya fice kamar iska yaja motarsa a guje yabar harabar asibitin ta kuwa zabura ta miqe zata bisa Dr Shattima yayi saurin riqeta ya hadata da jikinsa yace “tabbas kina cikin jarabawar ubangiji kamar yanda nake cikinta Habbatullah banyi tunanin wannan Ikcn zaizo ba kiyi hqr zuciyarki a kumbure take idan kika mutu bashida asara saboda saura kwanaki biyar ya angwance da sabuwar amaryarsa...........

_Gareku masoya garabasa gareku saboda murnar bikin babbar sallah daga yau 3/8/2020 zuwa_ _10/8/2020 na rage kudin da ake biya domin samun wannan_ _rikitaccen labari me cike da turka turka single Zaki biya 150 VIP 400 idan ta account ne._
_Account 0255526235 Fauziyya Tasi'u Umar GTB, saiki tura evidence_ _of payment ta wannan number 09013718241_
_Idan katine kuma Zaki biya 200 VIP 400  ta wannan number_ _09013718241 kada ki manta lambobin katin ake buqata ko hotonsa._
# *UMMUH HAIRAN*
[8/9, 4:07 PM] OPEN EYES MULTIMEDIA: *HABEEYTAH*
*_DUBAI PART 2_*

*FAUZIYYA TASI'U UMAR*

*UMMUH HAIRAN*

*7*

Zamewa tayi daga jikinsa ta zube a qasa numfashinta yana sarqewa ta dafe qirjinta jikinta yana rawa Dr Shattima ya matso da sauri ya kamata ya dorata a gadon ya zaro wata allura ya danna nata nandanan jikinta yayi laushi ta suma Granny ta juya ta kalli Saudat data zubawa Habeey ido cike da tsananin tausayawa hawayenta na zuba a qasa tace.
“Meye kuma abin kukan Saudatu kunyi nasara tabbas kuyin nasara Allah ya baku saa kun raba tsakanin Taheer da Habeey, Saudatu badai Taheer kikeso ba gakinan gashi daukar yarinyar dake bacci tayi ta miqa Mata tace “ga yar mijinki nan ki dauka ki riqe kwafi samun nutsuwa amma kafin wannan Ikcn inaso kisan wani abu qwaya daya ita duniya juyawa takeyi saboda haka kada kiyi tunanin dawwama cikin farin ciki kin rabashi da farin cikinsa kin yankewa Habiba nata farin cikin shakka babu Ikc na zuwa da zakiyi naki kukan babu hawaye"

Kubrah ce ta dubeta tayi “murmushi tace “haqqin rai biyu ne akanku Saudat koma nace uku saboda ke yaya yaci mutuncin Habiba saboda ke ya rabata da yarta saboda ke komai zai iya faruwa dashi kansa yayan, Abu daya nima da zan fada miki shine quncinki sai yafi wanda kika sanya zuqatan masoya sannan babu ubanda ya isa ya raba Safnah da mahaifiyarta harsai idan sune sukace bazasu riqe ba"
Addah ce ta girgiza kai tace ku bashi yarsa kawai bsmu buqata Allah ya rayata a duk inda take wannan qaddarorin na Habbatullah sinyi yawa Allah ka sassautawa baiwarka haka" hawayen saudat ne ya qara tsinkewa tace “wlh tallahi bansan meyene ya kawo wannan sauyin ba Granny yanzu kafin mu taho har zagina Yaya Taheer yayi akan Habeeytah ya rantsemin ya qara kan cewa koya aureni saiya sakeni ni zuwa nayi idan ta farka na roqeta ta nemamin alfarmar ya hadamu ya auremu"

Murmushin takaici Granny tayi ta juya zauna daidai Ikcn da Dr shattima ya sake shigowa yace “nan da 30 minutes zata iya farfadowa don Allah a kawar mata da duk wani Abu dazai sanyata damuwa" jinjina kai sukayi ya sake fita, haka kuwa akayi 35 minutes da fitarsa ta farka a firgice tana Kiran Taheer kada kayimin haka don Allah wlh nafi kowa sonka kada ka rabani da yata ita kadai na mallaka duk duniyar nan kada ka sanyama yata maraicin uwa a halin uwarta tana raye kada ka qara tabbatarwa da zuciyata namiji tuwon rezar ne miyar Allura ashe wannan ranar zatazo Taheer Kaine da kanka kayimin gori?"
Kuka takeyi Addah na riqeta tace “da nasan wannan ranar zatazo Dana roqi Allah ya kasheni kafin Ikcn, wayyoh Allah qirjina Allah ni yaushe zanyi farib cikine kamar kowa...."

Ta qarashe mgnr tans kakarin amai kamar zata amayar da kayan cikinta amma aman yana qara tsanani sai jini, wani ihu Addah tayi ta qanqame yar tata Saudat ta nufota da gudu itama ta riqeta tana kuka tace “nashiga ukuna Taheer kada kayi kisa don Allah ka dawo ka janye kalamanka Taheer asheni ba sonka nakeyi ba ga wacce take sonka..."
Daqyar cikin taimakon Allah Dr Shattima da Dr Zainab suka samu aman ya tsaya suka daura mata na'urar shaqar iska saboda Athmer dinta data tashi tanata gwama numfashi Dr Shattima cikin tashin hankali yaketa fadan ya akayi aka bari ta tuna abinda ya faru?

Wannan rana sunga ikon Allah dukkansu anan suka kwana akanta Kiran duniya Bushirah tayiwa wayar Taheer amma a kashe saita Dad ya Kira ta fada masa abinda yake faruwa shima ya shiga rudu saboda zuwa yanzu tausayin Habeey ya gama ratsa jikinsa yace su jirashi gashinan zuwa.
Haka kuws akayi jiransa sukayi bai dadeba ya iso.
Granny ce tayi masa bayanin komai ya zauna yana salati tare da tunanin mafita a fili yace “aikuwa saidai ya hada biyun ya aura wannan ma zalumcine ya gama lalata mata rayuwa sannan yace bazai aureta ba" da sauri Addah tace “aa kada ayi haka Alh tunda yace bayaso ku qyaleshi matar mutum kabarinsa qila dama ba matarsa bace" duk yanda Dad yaso yabawa Addah hqr ta tubure qarahema tace itafa indai ta isa da Habeey bazata auri Taheer ba.

Jikin kowa yayi sanyi Dad ya dauki takarda da biro yayi rubutu ya miqawa Addah yace “ku riqe wannan don Allah kafin a daidaita komai ina ganin Taheer ba a cikin hayyacinsa yake ba" girgiza kai tayi tace “bama buqatar komai daga gareku ranka ya dade iya hakama min gde Allah ya qara daukaka"
Daqyar ya roqeta ta karba check din kudin sannan ya debe yayansa suka tafi amma banda Bushirah da takejin ciwon abinda ya faru kamar ita akayiwa, sai dare Habeey ta farka ta bude idonta tana kallon silling din maganganun Taheer sunayi mata yawo a kwanya “ballagaza banza me zanyi da ita karuwar yarinyar nan..."

Wata qara ta saki Dr Shattima daya kasa ya tsare ya miqe da sauri ya isa gurinta ya fara dubata ya cire mata abin taimakawa numfashin da aka maqala mata ya zare mata allurar drip din yana Mata murmushi ita kuma sai kallonsa takeyi hawaye na zuba a idonta.
Zama yayi a gefenta yace “idan baki manta da komai kin fawwalawa Allah ba Zaki kashe kanki Habbatullah akwai darasi me yawa a cikin rayuwarki kuma ita qaddara bata shawara lkcn da zata fadowa mutum wlh a iyakar kwanakinki a asibitin nan bantaba sanin Taheer ba mijinki bane

sai kwanaki uku da mahaifiyarki tazo, shima waya naji tanayi tana kuka tana fadawa wata halin da kike ciki"

Shassheqar kuka takeyi ta yunqura zata miqe yayi saurin kamota ya tallafa mata ta zauna yace “kiyi hqr muyi addu'a Allah yayiwa kowa zabi na alkhairi amma ni dama nayi tunanin faruwar hakan ba yanzu bako a gaba"
Itadai batace komai ba har ya zauna ya zuba mata ido zuciyarta suya takeyi sosai qaddarorinta sun fara bijirewa kwayarta a firgice ta dago tace “ina yata?" Dago idanunsa yayi da suka kada sukayi jah tunda yake aiki baitabajin tausayin wata mace kamar yanda yake tausayin Habbatullah ba yace “babanta ya dawo ya dauketa kiyi Mata addu'a duk inda take zata isheta" miqewa yayi da sauri ya fice saboda zuciyarsa ta gama karyewa.

A cikin kwanaki biyun da suka qara sosai Addah da Granny ke qarfafa mata gwiwa tare da kafa Mata misalai da hujjoji da zasu sanya ta manta da Taheer a rayuwarta saboda juyin duniya Dad yayi dashi akan ya koma kodan safnah su daidaita da Habbatullah suyi aure Amma fir yaqi yace shifa baisan meye yasa masa tsanarta ba ko sunanta aka Kira gabansa faduwa yakeyi.
Ganin yanda ran Dad ya baci ne yasashi fadawa jikinsa ya fashe da kuka yana cewa “wlh Dad qasan zuciyata danqare take da qaunar Habeeytah amma jikina da ruhina tsanarta suke qarayi Dad bansan meye ya canzamin qaunar Habeeytah da tausayinta zuwa qiyayyarta ba, alfarma days zakayimin Dad kada ka daura aurena da Saudat wlh idan ka daura mutuwa zanyi kabarni na rayu da yata  ta isheni rayuwa nayi maka alqawarin kare kaina nayi maka alqawarin zan rinqayin azumin litinin da alhamis"

Lamarin ya fara girmamewa tunanin Dad duk yanda yake tunanin Taheer ya wucce nan kamashi yayi ya dagashi zuwa yanzu ya daina ganin baqin dannasa tausayinsa yakeji a sanyaye yace “bazan taba takura maka ka auri abinda ranka bayaso ba amma zamanka haka risk ne kayi hqr ka auri yar uwarka Saudat nasan zakaji dadin hakan a gaba Taheer inajin kunyar na kira sahabi na fada masa na fasa aurawa dana yarsa shi tunani yakeyi na isa dakai kayimin wannan alfarmar Taheer"
Miqewa yayi yana hada hanya ya shiga bangarensa ya fada gado yanajin qirjinsa yana zafi ya zubawa qaton hotonsa da Habbatullah ido yana kallon yanda suke cikin nishadi Ikcn da sukayisa yana kukan zucci qaunarta tana qwaqular qasan zuciyarsa amma ya kasa gane hakan yanda ya zuba mata ido yana kallonta har wani buda hannunsa yakeyi wai ta shiga qirjinsa.

Kwana biyu suka qara Granny ta rakasu har Gombe har sukaje Habeey na kwance a kafadar Granny zuwa yanzu ta daina kukan rabuwa da Taheer kukan rabata da yarta takeyi a sanyaye tace “don Allah Granny ki kawomin Safnah naganta nayi Mata addu'a Ina roqon Allah kada yakaita lkcn da zata dandani irin abinda ubanta ya dandanamin, Allah kaji qanta ka tausaya Mata kada ka juya sakayyar bataji ba bata gani ba a kanta Allah ka rayamin ita rayuwa me albarka, shikenan yanzu Granny bazan qara ganinta ba?"..….....

_Gareku masoya garabasa gareku saboda murnar bikin babbar sallah daga yau 3/8/2020 zuwa_ _10/8/2020 na rage kudin da ake biya domin samun wannan_ _rikitaccen labari me cike da turka turka single Zaki biya 150 VIP 400 idan ta account ne._
_Account 0255526235 Fauziyya Tasi'u Umar GTB, saiki tura evidence_ _of payment ta wannan number 09013718241_
_Idan katine kuma Zaki biya 200 VIP 400  ta wannan number_ _09013718241 kada ki manta lambobin katin ake buqata ko hotonsa._
# *UMMUH HAIRAN*
[8/9, 4:08 PM] OPEN EYES MULTIMEDIA: *HABEEYTAH*
*_DUBAI PART 2_*

*FAUZIYYA TASI'U UMAR*
*UMMUH HAIRAN*

*8*

Sosai kalamanta suka ratsa zuciyar Granny jin kukan nata takeyi kamar tana dora mata dutsi aqirjinta a hankali taci gaba da rarrashinta har suka isa gidan sukayi sallama da Granny akan cewa idan an gama biki zasu dawo suga yanayin jikin Habeey.
Tunda suka shiga ta qule daki taja bargo ta rufe jikinta sanyin zazzabi yana ratsata tana nunka nadamarta tanajin ninkin tsanar jinsin da namiji a zuciyarta, ashe dama muguntar da Taheer ya shirya mata kenan ya nace saita soshi saida ya koya mata sonsa sannan ya juya Mata baya ya rabu da ita rabuwa mafi ciwo a lkcn da tafi kowa buqatarsa.

Kuka takeyi sosai tana juyi a cikin bargon tana ambaton ya Allah tare da danna qirjinta son Taheer qila ita kuma shine ajalinta, a galabaice ta miqe ta sauko tana dafa bango ta shiga bandaki ta kama ruwa ta dauro alwala tazo ta tayar da sallar azahar tana kuka tana fadawa Allah damuwarta.
Bayan ta idar ta dauki qur'ani data gani a gefe ajiye ta fara karantawa tanajin sassaucin nauyin da qirjinta yayi bayan ta idar ta daga hannunta tana kuka kunyar ubangijinta takeji ta kasa bude baki ta nemi yafiyarsa gani takeyi kamar bazai dubeta da idon rahmaba.

Amma data tuna Allah gafuru al rahim ne sai taji sanyi a ranta ta fara neman yafiyarsa da zuciya me tsarki ta jima tana Istigfari sannan ta rufe qur'anin ta koma ta kwanta tunanin baya yana dawo Mata da irin alqawurran da Taheer ya rinqa yimata Ikcn da yana kwadayin jikinta.
Safnah tafi komai tsaya Mata a ranta tunanin kalmar da zata fadawa yarinyar Ikcn data girma taji irin hanyar da sukabi suka samar da ita takeyi.
Toshe bakinta tayi da hannunta saboda ita kanta tagaji da kukan da takeyi so take ta saba da wannan rayuwar data samu kanta a ciki saboda tasan itace qaddararta, Addah ce ta shigo da waya a kare a kunnenta ta zauna kusa da ita ta dafata tace “na fada miki banson damuwar nan da kike sanyawa kanki Habbatullah muyi hqr komai yayi farko zaiyi qarshe ga yar uwarki zakuyi mgn"

Kara Mata tayi a kunneta tayi sallama da murya me rauni Fatima tace “Yaya Habeey ya jikinki ince dai kin warke?" Ajiyar numfashi tayi tace “gangar jikina ta warke amma zuciyata zafi takeyi Fatima nafi buqatar mutuwa akan wannan rayuwar da nakeyi mara albarka na rasa farin ciki ta ko ina..." Saurin katseta tayi da cewa “ki daina wannan zancen Yaya wata rana sai Ibr don Allah kiyi hqr ki manta da wannan mayaudarin insha Allahu Allah zai saka miki"
Lumshe idonta tayi tace “don Allah Fatima ku dawo gda kada kiyi sha'awar yin rayuwa irin tawa babu komai a cikinta sai tozarci da qasqanci ki fito a kamoki ko ki bawa argent dinki number ta ya kirani na bashi kudinsa ku dawo mu nemawa rayuwarmu makoma, bana fatan rayuwarku ta lalace kamar tawa nikam nasan babuni babu farin ciki a rayuwata"

Jikin Fatima yayi sanyi matuqa sukayi sallama ta Addah ta dubeta ta kawar dakai tasani duk itace ta jefa rayuwar Habeey cikin wannan gararin, miqewa tayi a kasalce ta nufi nata dakin tana kukan zuci dana zahiri yarinyarta me biyayya dason faranta mata yau gata tana kuka saboda wasan da tayi da rayuwarta ta rabata da gatanta ta kawota ts hadata da muguwar rayuwar data zabawa kanta yanzu ta Yaya ma zata tunkari Salahu da mgnr wata ya dake tsakaninsu balle har ya karbeta ya a matsayin jininsa bayan an fada masa cewa cikin ya zube?

Hakanan suka yini a daki kowa zuciyarsa babu dadi sai yamma sannan Habeey ta qarfafa jikinta a qoqarinta na sanyawa kanta dangana da rungumar qaddararta ta fito tsakar gidan ta zauna Addah na gyaran kubewa ita kuma tana gyara Mata ganyen ugo saboda rashin wadataccen jinin da Habeey ke fama dashi shiyasa ta bayar aka siyoshi zatayi mata miya dashi.

Rayuwar Habeey da mahaifiyarta da yan'uwanta gwanin dadi cikin kwanaki ukun gata sosai suke nuna Mata basu barinta da damuwar komai ko yaushe cikin sanyata dariya suke, biye musu takeyi amma qasan zuciyarta ta kasa cire Taheer a cikinta kullum mafarkinta shine ko magana akayi mata wani Ikcn shi take ambato.
Lamarin da yake damun Addah itadai da gaske batason ko wani abu daya shafi Taheer so takeyi ya fita cikin qaddarar yarta har cikin ranta dadi taji days karbi yarsa, cikin kwanaki ukun ne Addah tasa aka ciro Mata kudin da governor Waziri ya basu kudine  ba kadan ba batare da kowa ya sani ba tasa aka nema mata babban gida na alfarma a cikin birnin gombe ta siya da sunan Habeey ta zuba musu komai na more rayuwa sauran ta dora jari sannan ta biyawa Habeey kudin wata babbar makarantar islamiyya.

Kwana daya suka qara sun gama shirinsu tsaf tace zasu rakata unguwa Habeey tana daki zaune tanata gwada wayar Taheer taqi tafiya sukaji sallamar mutane a tsakar gidan gaban Habeey ne ya fadi saboda tunaninta Dr Shattima ne saboda ya takura musu da ziyara cikin kwanakin nan.
Amsawa Idris da Ibrahim sukayi suka fita da sauri itama ta miqe ta fito sanye da hijjab dinta har qasa saboda dokace Addah ta sanya mata ta tsaya a bakin qofar dakin.
Shigowa sukayi ta dago kanta a dan tsorace saboda jin muryar Governor Waziri ta zuba masa ido gabanta na faduwa itadai kawai governor Waziri kama yake Mata da wani Wanda ta sani, a bayansa wasu mutum biyu ne sai Shattima dake biye dasu.

Janye idonta tayi dagakan governor Waziri ta saukeshi akan wanda yakebin bayansa shima ita yake kallo ga mamakinta sai taga kowa ya tsaya amma shi ya nufota tayi saurin rintse idonta kawai saijinta tayi a jikinsa ya rungumeta tsam ya fashe da kuka yana fadin.
“Itace wlh azeem Habbatullah yatace yayar Saudat ce Innanillahi wa innah ilaihirraji'un dama zanganta ashe mafarkina gaskiyane da yake nunamin zuwan wannan rikitaccen Ikcn meyesa Yaya meyasa kuka boyemin bayan kunsan inda take meye yasa baka sanar dani ba Saida aka daura auren Taheer da Saudat"............
# *UMMUH HAIRAN*

[8/9, 4:08 PM] OPEN EYES MULTIMEDIA: *HABEEYTAH*
*_DUBAI PART 2_*

*FAUZIYYA TASI'U UMAR*
*UMMUH HAIRAN*

*9*

Zamewa tayi a jikin Alh Sahabi ta zube a qasa summamiya Taheer dake shigowa ya hankade governor Waziri dake riqeshi ya fada kanta ya dagota yana jijjigata yana Kiran sunanta kawai shima sai ya zame a kanta zuciyarsa na harbawa da sauri, a haka Saudat da Bushirah suka shigo suka samesu.
Saudat ta sulale qasa cikin kuka me gunji tace "ni dama tun ganina na farko da Habibah nasan akwai wani abu tsakanina da ita wlh na hqr da Yaya Taheer koda soyayyarsa zata kasheni Dad dama tun kafin nasan da wannan jumurdar ya sakeni saki uku minti uku bayan daura aurena dashi...."

Salati Dad ya saki cikin sarewa zuciya ya qarasa gabanta ya riqota yace Alh Sahabi ya sunkuya ya janye Taheer daga jikin Habeey yace "hakan yayimin dadi ya burgeni sosai Saudat yayi abinda ya dace dama bansan da cewa bashi ya amince da aurenki ba da tun farko bazaayi sa ba" Addah ce ta shigo daga maqota data shiga sallama ta tarar da gdan cike da mutane da sauri taja baya saboda hada idon da sukayi da Sahabi tace "Salahu!" Da qarfi tayi mgnr ya kawar dakai tare da cije lebansa ya kinkimi Habeey ya fice da ita ya sanyata a mota zuciyarsa na bugawa da qarfi Alh Aminu da governor Waziri sune suka fito da Taheer sai Kubrah da Bushirah da suka kamo Saudat da taketa gursheqen kukan rabuwa da masoyi tasan Koda Taheer bai yanke igiyoyin aurensa da aka daura awa da suka wucce akanta ba to bayyanar Habeey matsayin yayarta shaqiqiya uba daya zaisa ta janye ta sallama Mata Taheer domin tafita buqatarsa tasani Habeey tafita son Taheer kuma sunmafi dacewa da junansu kasantuwar jinin dake gudanawa a jikinsu ma iri dayane.

Wani babban asibiti dakenan cikin garin gombe suka nufa Abba gudu yakeyi kamar zai tashi sama saboda a yanzu ji yakeyi kamar mutuwar Habeey mutuwarsa ce, suna zuwa ya qara sunkutarta ya nufi cikin asibitin da ita ma'aikatan suna ganinsa suka rinqa darewa suna bashi guri kasancewar asibitin kansa mallakinsa ne.

Shiga yayi da ita dakin agajin gaggawa yasa aka kira masa likitocin shima ya cire babbar rigarsa suka baje fasaharsu wajen ceto rayuwar gudan jinin nasa daya dade yana mafarkinta ya dade yana ganin surarta a baccinsa wannan rans daxai tsaya gabanta yana qoqarin dawo Mata da rayuwarta da take qoqarin qwacewa ta dade tana zuwar masa a baccinsa.

Sunfi awa biyar a kanta komai na jikinta saida aka cire Mata ya rage daga ita sai under siket hstta bra saida Abba ya balle Mata saboda kokawa sukeyi da numfashinta da yakeyin sama suna fincikoshi daqyar zuciyarta kuwa bugunta yayi qasa fiye da mizanin da ruhi zai iya rayuwa da  harbawarta.
Daqyar da taimakon oxygen suka samu bugun zuciyarta ya rinqa dawowa a hankali cikin abinda bai wucce daqiqa talatin ba ya dawo yanda zata iya rayuwar qila wa qala dashi, amma anyi rashin sa'ar shigarta commar da zata iya shekara guda a cikinta saboda duka jijiyoyin da suke kai saqon tunani qwanyarta sun tafi hutun wuccin gadi idan aka matsa musu dawowa zasu iyayin bombing gabadaya.

Wannan dalili ya tashi hankalin kowa dake cikin asibitin musamman Saudat da taketa kuka tana tsinewa son zuciyarta da yakaisu wannan matakin qiri² saboda rashin tausayinta da son kanta gashi ta jazawa yar uwarta tilo daya tal a duniya fadawa halin rai kwakwai mutu kwakwai wannan abu zai dade yana taba zuciyarta.
Shima bangaren Taheer yana cikin tsaka me wuya Amma shi da dan dama dama akan Habeey shi karo na farkone daya samu heart attack akwai yuwuwar nashi ya lafa da sauri.
Granny bata samu labarin abinda ke faruwa ba sai dare aikuwa a daren tace sai ankaita taga jikokinta, Ikcn da tazo Bushirah tana kuka take fada Mata halin da Habeey take ciki ta rinqa salati tana matsar hawaye tace.

“Ni dama tun ganina na farko da yarinyar nan nasa akwai wani boyayyen al'amari game da haduwarta da Taheer Allah shi kadai yasan abinda ya boye tsakaninsu yanzu gashi gaskiya ta bayyana Kuma dole dan baqin ciki yaji kunya wlh Koda Taheer bai saki wannan ja'irar yarinyar ba sai ubansa ya saketa kuma a daren nan ko Habiba zata mutu saita mutu matsayin matar Taheer a wannan daren zaa daura"
Hakan kuwa itace ta faru a wannan dare Granny ta gwada ikonta Hajiya tanacan gaho da baki aka daura auren Taheer da Habeey wannan abu yayiwa kowa dadi duk da daga angon har amaryar basusan abinda ake ciki ba.

Sai sha daya na dare Dad ya koma gda shida su Kubrah da Saudat ta take dauriya saboda wani mugun zazzabi daya rufeta, suna zuwa gda ta shige dakinsu taja bargo ta rufe jikinta tana rera kukanta a zahirin gaskiya ba kukan rashin Taheer takeyi ba saboda a yanzu tanajin so da qaunar Habeey fiye da kanta.
A haka Aunty Zahrah mahaifiyarta tazo ta sameta a kwance cikin halin jinya ta dagota ta bude idonta da suka kumbura saboda kuka tana ganin mahaifiyarta ta fada jikinta ta rungumeta ta sake qarawa kukanta sauti tace “nayi baqin cikin zamowata silar shiga tsakanin yar uwata da bani da tamkarta a duniya da masoyinta haqiqa gsky ne layu'alimul gaibu illallah wlh da ace nasan Habeeytah yar uwatace da banyi sakacin da soyayyar mijinta ta huda zuciyata ta shigaba yanzu gashi gsky ta bayyana nice a qasa"

Tana fadin haka ta sake fadawa jikin Aunty Zahrah tace “shikenan Taheer ya tabbata ba nawaba dama yasha fadamin shi na Habeeytah ne gara nabarshi tun kafin lkc ya sanya nabarshi ta qarfi yanzu gashi ta qarfin zan barshi aunty naga samu naga rashi ya sakeni saki uku minti uku da daura aurens dashi ya turomin text massage a baya na qudurce bazan fadawa kowa ba amma yanzu dole lkc yasa na fada harma an maye masa gurbina da yar uwata Habbatullah...."
Jijjigata Aunty Zahrah tayi tace “keni kin cikani da shirme wace Habbatullah?" Bushirah dake shigowa tayi murmushin jin dadi tace “uwar wannan yarinyar" ta nuna Safnah dake kwance a kafadarta tana baccinta taci gaba da cewa “dama qarya fure take bata yaya rabon gsky ta bayyana mu qara dangi ne yar uwarmu ta dawo garemu yasa har hakan ta faru ni na tabbata Koda ace auren nan ya dade to bazaa zauna lfy ba saboda zuciyarsa tana gurin uwar yarsa" ta juya ta kalli Mom tace “kema yau kaifin harshena bazai tsallakeki ba Mom an dade anayi Ina sanya ido to yau dai gsky ta bayyana Habeey da kike qi har kike shirka saboda ki rabata da danki itama jininki ce dake da Abba Sahabi abokan wasane da babansa da babaki uwa daya uba daya yanzu kije a zuqe jinin Abba Sahabi daga jikinki kinga shikenan kin huta mudai munason yar'uwarmu sannan aure Allah baiyi hadin naki ba nasa ya qullah Yaya Taheer ya angwance da amaryarsa Habibatullah dan baqin ciki saidai ya mutu Safnah zata tashi cikin gatanta ta zama yar gata haihuwar dangi duk wanda ya zagi uwarta kansa ya zaga ka zagi ubanta ka gingimo dutsin dala dabara ta rage take Mom nidai shawara na baki kiyi maza kije a zuqe miki digon jinin Dad da Abba Sahabi a cikin jininki"................
# *UMMUH HAIRAN*
[8/9, 4:08 PM] OPEN EYES MULTIMEDIA: *HABEEYTAH*
*_DUBAI PART 2_*

*FAUZIYYA TASI'U UMAR*
*UMMUH HAIRAN*

_Please ki biya kafin ki karanta,daganan zuwa 10/8/2020 VIP 400 single 150, account 0255526235_
_Fauziyya Tasi'u Umar GTB idan katine ta wannan number 09013718241 hoton katin Zaki tura ko lambobinsa ta wannan number dake sama idan ta account ne Zaki tura evidance of payment dinki ta number dake sama._

*10*

Dafe qirji Mom tayi tace “Nashiga uku ni Safinah Bushirah me kike cewa ne wlh qwanyata ta tafi hutu bana gane komai" tabe baki Bushirah tayi ta dauki Pampers din baby Safnah ta fice tana cewa “kanku dai akeji aure Allah yayi alqawarin Habibah ce matar Yaya Taheer sai ku hadiyi zuciya ku mutu ku huta"
Binta sukayi da kallo har ta fice kalma daya ta kasa fitowa daga bakinsu Mom ta zube a gurin dabar tare da Dora hannunta aka ta zunduma ihun days firgita kowa suka sake yowa dakin da sauri, zare idanu takeyi tana kallon kowa ta cafki hannun Kubrah tace “me...meye yake faruwa Kubrah don Allah fadamin me ake Shirin yimin ne"

Dariya tabawa Kubrah tace “mom kema da abin haushi kike to meyene kuma alqawarin Allah ne ya cika Taheer mijin Habbatullah kinqi Allah yaso ya qulla abinsa yabarki da kunya amma Mom ai kina da wani dan ki hadashi da wannan yarinyar mana, dama ai gadon ari sai fanna"
Miqewa Aunty Zahrah tayi tana sharar hawaye tace “ashe dama wulaqancin da kuka shirya yimin da yayanki kenan Yaya Safinah kuka matsa saida muka baro England mukazo 9ja, tur wlh kin bani kunya ashe isar taki ta banzace baki isa da danki da mijinki ba Yaya kinbani kunya nayi nadamar zama qanwarki tunda kin kasa cikawa tilon yata burinta data rayu dashi tun quruciya har kawo girma"

Fincikar Hannun Saudat tayi tace “duk Dan daya hana uwarsa bacci to yasa a ransa shima bazaiyi ba zan dauki mataki farin ciki dai Taheer bazaiyishi bs kamar yanda ya hanamin yata ta warwasa"
Riqeta Mom tayi tace “kada muyi haka dake Zahrah ki muje dakina mubi komai a sannu fadan ya canza salo halan ke baki fahimci ma abinda suke cewa ba, to bari nayi miki bayani wannan karuwar yarinyar da nake fada miki Lele ya mutu akansa ta tsaface zuciyarsa ba kowa bace face yar Hajar matar Alh Sahabi ma'ana babbar yarsa da muka kashe maqudan kudade dan batar da babinta cikin rayuwar zuri'ar Maje Bauchi"

Wani mugun tsoro ne ya kama Zahrah ta zame qasa cikin tashin hankali tace “nashiga ukuna Yaya ai ban fahimci abinda yake faruwa ba dama ashe bata mutu ba Mal yacemin zai batar da ita a duniya zata lalace sannan daga baya a yawon barikinta ta dauko abin kunya ta jajubo cutar qanjamau ta mutu ashe duk qarya yayimin"
Rufe mata baki tayi Ikcn da Dad yake shigowa ya bisu da kallo Mom tayi saurin miqewa tace “dama yanzu nake shirin kiranka Dad kaji abinda yaron nan yayi mana minti uku da daura aurensa da yar'uwarsa Saudat ya rattaba mata saki uku?"

Kallon inda Saudat take nade yayi yace “haka Allah ya tsara muma godewa Allah da abin ya tsaya iyanan da baiyi hakan ba da abin ya rikice mana ashe yarinyar nan Habbatullah yayar Saudat ce ubansu daya kinga kuwa ai da anyi abin kunya duk da kasancewar aure ya halatta tsakanin Saudat da Taheer tunda a baya ba auren Habbatullah yayi ba Amma ai ana barin halak ko don kunya musamman da yake Taheer ba Saudat yakeso ba Habbatullah yakeso"
Girgiza kai Mom tayi tace “Lallai kam da anyi abin kunya to Allah yasa hakan shi yafi alkhairi yanzu Ina suke ance kun dora auren ko?"

Jinjina kai yayi yace “Granny dinsu ta tursasa aka daura auren tace Koda dayansu zai mutu saidai su mutu matsayin ma'aurata" wani mashi ne ya sake sukar maqoshin Mom amma sai tace “hakanma yayi yanzu ina suke?" Cikin jin dadin yarda Mom ta Basu hadinkai governor Waziri yace “a halin da ake ciki ita Habbatullah jin cewa Taheer ya zama mijin qanwarta yasata yanke jiki ta fadi qanwar matacciya a fadar likitoci sunce zata iya daukar watanni goma a wannan halin na doguwar suma shikuwa Lale ya samu heart attack yanzu haka yana samun kulawa daga likitocin asibitin Sahabi dake gombe amma akwai yuwuwar zaa tafi dasu England acan zasufi samun kulawa"

Cikin tashin hankali Mom tace “taheer din yanzu Kuma mutuwa zaiyi don Allah Dad ayi duk abinda ya dace" miqewa yayi yace “insha Allahu zasu tashi suyi rayuwa me tsayi sai sun Haifa mana halattatun jikoki, Ina Safnah yau banganta ba"
Tabe baki tayi tace “tana gurin iyayenta" sai yanzu ya tuna da yayan nasa mata duka matsayin matan wasu suke, yace “Subhanallahi meye ya hanasu tafiya gidajen mazajensu bayan an gama komai"
Itadai bata bashi amsa ba ya juya ya fice yayi niyyar tasosu yakai kowacce gdan mijinta Amma sai yaga har shabiyu na dare kuma Basu gama bidi'arsu ba.

Kallon Mom Zahrah tayi tace “shikenan burinsu ya cika na yata ya wargatse haka kike nufi Yaya?" Dafata tayi tace “har yanzu akwai quruciya a jikinki Zahrah idan rawa ta canza dole kida canzawa yakeyi kuma Shirin zaune yafi na tsaye a yanzu nuna qiyayyarmu ga yarinyar nan baqin jini zaija mana musamman ke, sakin ranmu zamuyi mu nuna komai ya wucce in yaso sai mu koma gefe mu sake shiri, ai wlh tunda na rantse banasonta bazan taba sonta ba sufa maza basu da tunani saboda haka mu bisu da yanda sukeso sai muci galaba akansu"

Haka suka rinqa tattaunawa har Hajiya Ummah yayarsu saida suka taso suka fada mata abinda yake faruwa, tayi dariya tace “kuma tanan suka bullo? Hmmm ku bar yan iska zamu iya dasu badai a kwance take ba to kuwa a haka zata qare rayuwarta saidai suyita asarar kudinsu a banza amma bazata tashi ba"
Dubanta Zahrah tayi tace “amma Yaya Ummah sai naga kamar yayi tsauri jinya tanada cin zuciya da jiki mudai nemi wata mafitar wannan batayi ba" hararta Mom tayi tace “bantaba yin tsafi ba sai akan shegiyar yarinyar nan nifa wlh yanda nakejin tsanarta da zata mutu ma da zanfi kowa farin ciki, Yaya Ummah shi Kuma wannan gardamammen yaron ya zamuyi dashi?"

Shiru tayi tana tunani sannan ta dago tace “kada ki damu dashi a barshi ya samu Ify ya warke qalau ita kuma a qara dora Mata jinya kuma ki tubure kice saidai a bashi ita yaje yayi jinyar matarsa ta hakane kawai zai fara nadamar bijire miki saboda zaiso kusanci da iyalinsa babu dama zaiso shima yaga matarsa a cikin halin Ify daga haka zai fara tunanin mafita zai fara danasanin aurenta zaiji tsanarta zai fara tunanin qara aure to daganan ne zamuyi amfani da wannan damar mu sanyashi sakinta sai mu maye masa gurbi da Saudat kinga shikenan ciki Ify baka Ify idan ta warke saita dauki jaka ta koma bariki Ikcn komai ya kankama tsakaninshi da Saudat qila ma ta haihu kinga aure ya haramta tsakaninsu indai ba mutuwa Saudat tayi ba"

Wani ihu Mom tayi tace “shiyasa nake sonki kanki naja Yaya Allah yabar mana ke" murmushi Zahrah tayi itadai har yanzu da sauran imani a ranta amma ya zatayi bata da wata hanyar ceton yarta saita amince da wannan gurguwar shawarar.
Miqewa tayi ta matsa ta taba jikin Saudat da tayi baccin wahala jikinta zum da zazzabi, gyara Mata bargo tayi ta kwanta a kusa da ita tana shafa kanta tana tausayawa tilon yar tata tasan zafin rashin masoyi tun akan Abba Sahabi Ikcn daya gujewa aurenta yaje ya auri Hajar, tana tuna irin azabar data rinqaji a heart dinta tana tunz irin wahalar da gangar jikinta ta shiga a Ikcn, hawaye ta share tace badan wata kusan tafi wata ba da bazan bari a cutar dake ba Habibah duk da kasancewar harda sanya hanuna a lalacewarki amma bayyanarki da abubuwan da suka faru sun sanyayamin jiki Ikcn da Yaya Safinah ta shigemin gaba wajen bata rayuwarki sai ya

kasance kuma da gudan jininta kuka lalace ita ta tsarawa boka tanaso kiyi cikin shege yanzu gashi ita zata goya yar da ta assasa zuwanta duniya tabbas akwai matsala gaba bamusan meye zai faru ba, Amma Kuma ni Yaya zanyi da tawa yar idan naqi basu hadin kai"...............
# *UMMUH HAIRAN*

[8/9, 4:08 PM] OPEN EYES MULTIMEDIA: *HABEEYTAH*
*_DUBAI PART 2_*

*FAUZIYYA TASI'U UMAR*
*UMMUH HAIRAN*

_Please ki biya kafin ki karanta,daganan zuwa 10/8/2020 VIP 400 single 150, account 0255526235_
_Fauziyya Tasi'u Umar GTB idan katine ta wannan number 09013718241 hoton katin Zaki tura ko lambobinsa ta wannan number dake sama idan ta account ne Zaki tura evidance of payment dinki ta number dake sama._

*11*

Haka kwanaki suka rinqa turawa kwanan Taheer biyar a kwance ya fara samun sauqi tunda ya farfado habeeytah kawai yake kira wani lkcn har sai an hada masa da Allurar bacci sannan yake samun nutsuwa, cikin kwanakin zuciya da jikin Mom sunqi hutawa duk inda zasu shiga su fito sun sun shiga.
Itadai Zahrah burinta a sake mantar da zuciyar Abba Sahabi Habeey Amma abin ya faskara qarshe bokan nasu da suka bawa amanna ya sanar da ita indai ta cika matsawa zata bata gomanta daya bata gyaruba dole ta hqr sukabar lamarin tsakanin Habeey da Taheer.

Kudi ba qanqana ba Mom ta kashe akan lallai a cusawa Dad aqidar qin bijirewa mgnrta haka kuwa akayi cikin lkc qanqani take juya ragamar governor Waziri.
Kwanaki goma Taheer yayi ya samu sauqi sosai zuciyarsa wasai da kyakkyawan albishir din da Dad yayi masa na musanya masa Habeey a matsayin matarsa farin ciki a gurinsa kamar zai zauce, Saida ya gama murnarsa da kukan dadinsa sannan yace “yanzu Dad tana Ina koma kun gama bikinku ban sani ba ankaimin ita gdana?"
Shafa kansa Dad yayi yace “kayi har an samu matsala lkcn da Habeey taji labarin an daura aurenka da Saudat ta yanke jiki ta fadi har yanzu batasan waye yake kantaba tana tsakankanin mutuwa da rayuwa Taheer likitoci sun tabbatar mana cewa bazata farfado ba sainan da watanni goma...."

Katse Dad yayi da cewa “what Dad! Kuma shine kuka tsaya kuka zuba Mata ido saboda bakusan ciwonta ba so kuke ku kashemin mata haba Dad haba Dad yaushe zaku fara daukan Habeeytah a matsayin da kuke daukar sauran yayanku...."
Shigowar Abba ne yasashi yin shiru Abba ya dafa Taheer yace “kayi hqr Granny ce ta takura Saida aka daura aurenka da Habeey a halin tana cikin jinya, Taheer naso ace sai Habeey ta warke akayi bikinku kukayi farin ciki kamar kowacce amarya da ango"
Girgiza masa kai yayi yasa hannu ya share masa qwallarsa Ikcn da tasa take saukowa yace “inason ganinta Abba ka rakani naganta don Allah"

Miqewa yayi ya nufi qofa Abba da Dad suka miqe suka rufa masa baya har dakin da Granny take jinyar jikanyar tata ya tsaya a bakin qofar ya zuba mata ido yana hawaye ya rinqa jan qafarsa a hankali har ya qarasa gadon ya durqushe a gabanta tare da kama hannunta yana kallon na'urorin da aka daddaure qirjinta dasu.
Wasu hawaye masu dumi suka kwaranyo masa suka zuba a saman hanun Habeey ya sake rungume hannunta a qirjinsa cikin kuka me sauti yace “rayuwata dake a haka tafimin dadi fiye da na rayu da matan duniyar nan Habeeytah ko tausayawa masoyinki me qaunarki domin Allah kada ki yankemin farin cikina wlh nayiwa wannan rayuwar tanadin farin ciki me dorewa har abada Habeeytah nayi alqawarin da sanina bazan qara sanyaki zubar da hawaye ba duk ranar da kika zama mallakina, ki tashi Habeeytah don Allah ki tashi kamata yayi ace a daidai wannan Ikcn muna kwance a dakinmu ne a gadonmu na sunnah kina kwance a qirjina Ina shafa wannan dogon gashin naki"

Yakai hanunsa ya shafo gashinta dake baje saman pillow wanda kullum sai Granny ta gyara matashi sai sheqi yake baqi sudik dashi, ya shagala sosai da kallonta da shafa sumar tata ya zubawa dan qaramin bakinta da smile face dinta idanu gani yakeyi kamar murmushi takeyi masa ya dago ya kalli Abba yace.
“Zo ka gani Abba murmushi takeyimin don Allah ka fada Mata karta mutu akai gift din da nakeson bata wacce na siyeta tun ranar farko dana fara saninta mace, na ajiyeta a matsayin kyautar da zan bata duk ranar data zama mallakina Abba ka fada mata da hannunta nakeson ta karba don Allah"

Ba Abba da ciwon yar tasa yakecin zuciyarsa ba hatta likitar dake kula da ita kuka takeyi cike da tausayin Taheer din tunda take bata taba ganin kojin Ibrn irin wannan soyayyar ba, Tasha ganin irin wannan usue din da zarar namiji ya fuskanci mace batada amfani a gurinsa zubar da ita yakeyi Amma shi yanzune ma ya fara sonta itakam zataso jin mafarin wannan sarqaqqiyar qaunar.
Da wannan tunanin ta dafashi tace “kayi hqr zata warke insha Allahu saita haifa maka yan biyu munzo Bauchi munsha suna yallabai" miqewa yayi yace “na gode Dr amma ya kamata kema kiyi wani taimakon wata goma yayi yawa inajin tausayin matata ni banida matsala wlh ko a haka zata dawwama zan zauna da ita zan sallama Ikcna wajen kula da matata"

Dafashi Dad yayi yace “dama jiran warkewarka mukeyi zaku tafi Germany na tanadar muku gdan da zaku zauna da likitan da zaike kula da ita gdan kusa da Royal hospital Germany yake daganan likitocin zasuke zuwa dubata ga kuma abbanku kusa daku"
Granny ce tayi saurin cewa “anya Aliyu wannan tsarin babu wauta a cikinsa jinyar mace sai mace kuma yaushe ma zakace zaka bawa Taheer wannan yarinya ya tafi da ita shi kadai nidai wannan shiri bai kwantamin ba"
Shigowa Mom tayi itada Zahrah tayi saurin cewa “wannan tsarin kwata[2] baiyi ba shima Taheer din ai zai iya kula da matarsa gsky bazasuje ko inaba kabarta anan yake kula da matarsa ga qanwarta nan saita zauna tare da ita"

Saurin kallonta Saudat tayi ta qifta Mata ido ta juya ta kalli Taheer ya zabga mata wata uwar harara yace “amma dai sainaji kamar baa sanyaki cikin maganar nan ba ko" daga masa hannu Dad yayi yace “hakan zaayi Taheer kawai a hqr da tafiyar nan tunda zatazo da matsala ko ya kagani Salahu?"
Jinjina kai yayi yace “duk yanda kukayi ma daidaine amma Saudat bazata gidan Habbatullah ta zauna ba kamar yanda na datse duk wata alaqa ta kusanci tsakanin Habbatullah da mahaifiyarta Hajar haka na datseta tsakanin Saudat da Habeey harsai zuwa Ikcn data samu sauqi dakanta ta nemeki kinji ko?"
Daga Kai tayi cikin qunar zuciya tace “naji Abba Amma..." Daga mata hannu yayi yace “kune musabbabin faruwar koma saboda haka banson jin komai daga gareki Taheer ka kula da matarka Allah ya taimaka maka zan nemo muku yan aiki biyu da zasuke tayaka jinyarta"

Murmushi yayi yace “na gde Abba amma bana buqatar tallafin kowa wajen kula da matata zan iya komai nasani idan nine a irin wannan halin Habeey bazata taba yarda wani ya kula dani ba

ita zatayimin komai saidai idan fin qarfinta akayi"
Sosai zuciyar Abba tayi sanyi yaji dadin kalaman Taheer duk da yasan hana tafiya da Habeey din wani salon makirci ne saboda sarai yana hango qiyayyarta a idanun Mom da matarsa Zahrah.
Itakuwa Saudat a duk lkcn da taga yanda Taheer yaketa jagwalgwala Habeey sai taji wani shauqi yana shigarta duk da tasan cewa yayi Mata nisa amma ta kasa daina kallonsa da fuskar qauna inda shi Kuma bata hangen komai a idonsa sai qiyayyarta.

Ran Mom baiso hakaba taso aja maganar har rai ya baci amma sai taga akasin haka suka fice zuciyar kowa babu dadi suka nufi gida Mom ta daki sitiyari tace “wannan abin yana firgitani anya kuwa Taheer mutum ne"
Tabe baki Saudat tayi tace “to wai Mom meye yasa kika tsani Aunty Habbatullah ne nifa indai danni kike wannan abin kima daina nariga na sallamawa yar'uwata mijinta dama tun farko rashin sanine yasa nayi yunqurin shiga tsakaninsu, Mom abin yayi yawa da wanne zasuji ne sunason juna kuka cusa musu tsanar juna lkcn da muke tunanin haqanmu zai cimma ruwa lkcn ne kuma Allah ya zartar da nasa hukuncin ya qullah auren da bakwaso...."

Wani bugu Zahrah takaiwa yar tata tace “shashasha mara kishin kai dama ashe kema haka kike inata kashe kudina don ginaki ke kina qoqarin rusani to wlh kika sake tausayin wannan makirar yarinyar ya ratsa zuciyarki sai ta rabaki da duk wata fada da kike taqama da ita uban naki ma saiya daina kallonki"
Shiru tayi batace komai ba qasan zuciyarta yana tunano mata yanda taga Taheer yana shigewa jikin Habeey tayi saurin kawar da tunanin ta dauki wayarta tana wasa da ita har sukazo gdan.
Kwanaki biyu Habeey ta qara a asibitin aka sallameta zuwa gda Taheer yaso su tare a gdan da Dad ya mallaka musu amma fir Dad yace saidai ya bari idan matarsa ta warke saisu tare, hakanan badon ransa yasoba saidon nasihar da Abba sahabi ya rinqa yi masa, shine dalilin da yasa ya hqr ya zauna a cikin government house din bangare guda aka ware musu aka zuba musu yan aiki sosai....
# *UMMUH HAIRAN*
[8/9, 4:08 PM] OPEN EYES MULTIMEDIA: *HABEEYTAH*
*_DUBAI PART 2_*

*12*

Ranar da suka tare kwana yayi yana kallonta yana hawaye yau ga Habeey dinsa yar uwarsa

jininsa matsayin matarsa amma saidai ya kalleta.
Miqewa yayi ya dauro alwala ya tayar da sallah yana kuka yana nemawa rayuwarsa lafiya gurin Wanda yake da ikon canza al'amura  sai asuba ya kwanta bacci ya dan daukeshi yana rungume da ita yanajin dumin jikinta na ratsashi.

Takwas ya tashi ya zuba Mata ido yana murmushi ko yaushe a kowanne hali fuskarta bata rabo da annuri ya share hawayensa ya sunkiyo daidai bakinta yace “kinaso nayi miki wanka?" Zuba mata ido yayi kawai sai yaji kukansa yana qara qarfi ya kwantar da kansa a jikinta yana lasar jajayen lips dinta da suke kullum kamar tasanya musu jambaki.
Dagata yayi a hankali ya cire mata komai dake jikinta yanajin faduwar gabansa na tsananta, ya dade yana kallonta daqyar a galabaice ya dauketa ya shiga da ita bathroom ya sanyata a ruwan wankan daya hada Mata ya diba ya watsa Mata a fuskarta duk ta rame yayi murmushi yace “nasan zakiso ramawa ko?" Diba yayi ya watsawa kansa yayi dariya yace “komai kikeso sh izanyi miki ko kaya zansa sai wanda nasan zakiso HABEEYTAH"

Yanayi mata wankan yana wasa da jikinta yanajin feel dinsa na qaruwa daqyar ya gama yimata wankan hakanan yaji yana sha'awar ya daura Mata alwala yayi Mata alwala ya daukota ya bude cikin wardrobe ya zubawa wardrobe din ido kayansa ne da nata a jere komai sabone yayi ajiyar zuciya wannan yasan aikin Abba Sahabi ne.
Wata baqar doguwar riga ya dauko ya juyo ya wareta ya kalleta yace “kinasonta baby?" Zuba Mata ido yayi sai kuma ya ninketa ya mayar yace “nasan bakison baqin kaya bari na dauko miki ja" wata jar doguwar riga ya dauko ya bude wata wardrobe din ya dauko jajayen band da dankunne fashion shima ja ya dawo ya ajiye ya dauko wasu mayuka masu masifar kyau da tsada ya matsa ya shafa mata ya taje Mata kanta a hankali sannan ya sanya band din ya daure mata ya kama jelar gashinta ya tufke kamar yanda yaga tanayi masa.

Kayan ya saka mata ya fesa mata turare ya koma gefe yana kallonta yana ajiyar zuciya tare da murmushi yace “Rayuwata inasonki" shima wanka yayi ya dauko wani blue din jeans yasa ya dauko jar riga yasaka ya kalleta yace “nayi miki kyau My life?" Murmushi yayi ya matsa ya lakace mata hanci ya fita yana cewa jirani na dauko alluranki..."
Turus yaja ya tsaya ganin Mom dinsa a tsaye a parlourn ita da Saudat ya kallesu a wulaqance, a zahiri kallonsa ne a haka indai ba saninsa kayi ba zakace tsabar iskanci ne, jikin Saudat rawa ya fara yasa hannu ya karbi Safnah dake hannunta yace “lafiya da safen nan?" Yanda Mom taga yanayinsa babu damuwa da Kuma kalaman da taji yana furtawa ya fadar Mata da gaba amma saita dake tace “dama munzo ganin jikin matar takane" murmushi yayi daya bayyanar da kyawawan haqoransa yace da sauqi fa sosai shiga ki ganta Mom har kwalliya nayi Mata".......

# *UMMUH HAIRAN*
[8/9, 4:09 PM] OPEN EYES MULTIMEDIA: HABEEYTAH
*_DUBAI PART 2_*

*13*

Zaro ido Mom tayi tace “kwalliya kuma gawar kayiwa kwalliya?" Tsuke fuskarsa yayi yace “aa Mom banason ki qara cewa matata gawa qila saima ki mutu ki barta waike meye yasa kullum bakinki baya taba fadin alkhairi akan matata ne nifa banson irin haka wlh rai zai iya baci"
Sakin baki tayi tana kallonsa har ya gama fadansa ya juya ya koma dakin ya kwantar da Safnah kusa da mahaifiyarta ya miqe domin fitowa suka hada ido da Mom ya sake tsuke fuskarsa yace “banason a dameta muje parlour" murmushin takaici tayi tace “indai wannan hoton hotiho dince da kanka zata isheka Taheer tunda ta zama Liability komai sai kayi mata"

Ko sauraronta baiyi ba ya dauko feedar Safnah ya zauna ya daukota yana Mata wasa ya hada mata madara ya jorner mata ganin bashi da niyyar basu guri yasata cewa da Saudat “ki zauna ki tayashi aiki"
Dagowa yayi ya watsa mata wata uwar harara ya mayar da kansa wa yarsa har saida Mom ta kusa ficewa daga dakin yace “dallah malama ki bacemin da gani anan banza mayya uwarki zaki tsaya kiyimin nida matata sai ansamin ido idan wani abin nayi niyyar yimata jiya da ubanwa muka kwana"
Tsorone ya kama Saudat tasan tana cewa wani abu jibgarta zaiyi ita ta rasa Ina Taheer ya kwaso wannan baqar zuciyar tasa, bin Mom tayi da sauri har ta fita ta dawo tace “am Yaya Safnan fa?"

Wata uwar tsawa ya daka Mata yace “uwarki ce ta haifamin ita da yazama dole na baki ita?" Wasu hawaye ne masu zafi suka zubo mata tace “amma dai Yaya kasani yar yar'uwata ce nima inada haqqi akanta..."
Wani kallo da yayi matane yasata ficewa da gudu ta nufi bangaren Mom din tana zuwa tayi kicibis da Mahfuz ya daka Mata tsawa yace “ubanme kike yiwa wannan uban gudun ballagaza kawai kizo ki shirya ni bazan iyada da zafin 9ja ba komawa inda na fito zanyi bandama su Dad da abinsu wani ni zaace na tafi dake ke wlh bama zan tafi dakeba kawai kice musu na tafi"
Yana gama fada Mata haka ya juya ya fice da sauri ta tabe baki tace “banza a banza duk izzarka baka kama qafar Hussain dinka ba, batakai nakeyi ba"

Shiga ciki tayi ta fara hada kayanta tare da cin alwashin ba zata qara kwana uku a 9ja ba ko su Abba bazasu koma ba ita zata tafi,
Itakuwa Mom tana shiga dakinta ta dokawa Hajiya Ummah waya tace “gsky Ummah banga alamun nasaraba shegen yaron nan bazai sare ba wlh bakiga yanda yake rawar qafa akan yarinyar nan ba abin haushin iyayensa sun daure masa gindi duk wasu shagunansa Dad ya sanya yaransa a ciki zasuke juya masa dukiyarsa sannan har wani albashi ya yanka masa hatta mara lfyr saida ya yanka Mata salary"

Dariya Ummah tayi tace “shine me da har zai sanya ki sare Safinah yau da gobe fah sai Allah wlh dole sai Taheer ya gaji da jinyar yarinyar nan Kuma duk ke kika bata abin aida kin bari sun tafi wajen inda babu wanda zai taimakeshi da komai"
Shiru tayi tana tunani kafin tace “Germany fah zasu tafi nafiso su tafi inda basuda kowa..."
Katseta tayi da cewa “ki aiwatar da aikin da aka baki kawai kice da Excellency ya kadasu su tafi acen din komai zaifi tafiya daidai kuma kada ki yarda a bar miki yarinyar nan ya tafi da kayarsa kinga itama qarin wahala ce"

Dake lusara ce haka ta yarda cikin farin ciki ta rinqa gudanar da al'amuranta cikin dare ta tashi batare da kowa ya ganta ba ko tsoron girman gdan bataji ta shiga bangaren nasu Taheer tayi saa ko lkcn daya fito zai raka likitan Safnah ta fara kuka ya koma da sauri bai dawo ya rufe ba bayan yayi Mata wanka ya hada Mata madararta ya bata ya dorata a kafadarsa tayi bacci ya kwantar da ita a gadonta ya koma ya daga Habeey ya gyarata yayi mata wanka ya dawo dawo da ita ya kwantar da ita.
Shima ya gaji saboda haka yana kwanciya bacci ya daukeshi har cikin ransa yafi tausayin Abba Sahabi fiye dashi kansa saboda yanda duk ya susuce akan ciwon na Habeey yau sun dade dashi suna tattaunawa akan ciwon yana cewa dashi yana shirya musu tafiya Saudia Wani Islamic Hospital akwai abokinsa acan yace yawanci irin wannan ciwon biyu ce take haduwa kodai tanada junnu a tare da ita ko kuma an jefeta dasu abin ya tadda ciwon, saboda haka Dr Manzir ya bashi shawarar a kawota nan a dorata akan magungunan Islamic.

Yaji dadin shawarar ta Abba Amma yace da abban yayi Shiru harsai komai ya kammala na

tafiyar, nan Abba yake fada masa cewa mahaifiyar Habeey dinma batada Ify cikin dare aka jita tana ihu kamar mahaukaciya tun daga Ikcn itama ta daina magana saidai kallo kawai ta kwatance Kuma bama kowanne mutum take ganewa ba yanzu haka tana Ɓillire gidan mahaifinta anata sauke mata qur'ani.
Jinjina kai Taheer yayi yace “amma lamarin da daure kai kuma Ina mijinta da yayanta maza da sukayi saura?" Girgiza kai Abba yayi yace da Taheer “tun ranar data tashi da ciwon da safe kafin kowa yazo kanta akace yazo ya tattare yayansa maza ya tafi dasu har jiya baa qarajin duriyarsu ba" da wannan tunanin bacci ya dauke Taheer nasararsa daya shi ko bazaiyi nafila ba baya kwanciya babu alwala Kuma ko iskancinsa yayi daya gama yake wanka wannan dalilin yasa hatta Habeey da batasan waye a kanta ba sai ya daura Mata alwala duk Ikcn da zaiyi sallah.

___________Itakuwa Mom tana shigowa ta kunna turaren tsafinta ta banka a parlourn ta tsaya idanunta a rufe hayaqin yabi ta qasan qofar dakin ya shiga daidai Ikcn Taheer yana saman sallaya yayi sujjadah yana nemawa matarsa sauqi gurin me duk.
Bajewa hayaqin yayi sannan ya nufi jikin Habeey dake kwance kamar gawa ya rinqa kewayeta abin mamaki hikima ta ubangiji Taheer yana cikin sujjadar nan kawai sai yaji motsi a saman gadon ya dago da sauri yayi tahiya yayi sallama yanajin Motsin na qaruwa baidai juya ba tunaninsa Safnah ce ta tashi.
Ji yayi anyi attishawa hakanne ya basa damar dago idanunsa da sauri ya saukesu akan gadon kawai sai yaga Habeey ce take motsawa bakinta yana furta “ LA'ILAHA ILLALLAH MUHAMMADUR RASULULLAH SALLALLAHU ALAIHI WASALLAM,  ASHHADU ALLA'ILAHA ILALLAH WA'ASHHADU ANNA MUHAMMADUN  ABDUHU WARASULIHI".........
# *UMMUH HAIRAN*
[8/9, 4:09 PM] OPEN EYES MULTIMEDIA:    *HABEEYTAH*
*_DUBAI PART 2_*

*14*

Da sauri ya miqe ya Isa inda take ya durqushe ya kama hannunta cikin matsanancin mamaki da murna yace “Habeeytah! Kece kin tashi? Da gaske kece kika tashi wayyohh Allah na Habeey alhmdllh ya Allah"
Duk wannan surutun da yakeyi bata bude idonta ba sai yanzu taketa qoqarin bude idon tare da son tuno wani abu game da ita, muryar data janyo mata faduwar itace ta rinqa dawo mata.
Ta yunqura da azama zata miqe sai taji gabobinta kamar baa jikinta suke ba ta bude idonta a hankali ta zubasu akan Taheer da yake tsugunne gabanta yanata kallonta hawayen farin ciki

suna zubo masa.

Ganin tanata kokawar tashine yasashi miqewa da nufin taimaka mata ta tashin amma ga mamakinsa sai yaga ta girgiza masa kai, ya saki baki yana kallonta har ta samu ta motsa daqyar ta dan muskuta daga inda take.
Zama yayi a kusa da ita yace yace “ki bari in tasheki inkira likita ya dubaki idan babu matsala saina nema miki abinda zakici" sake Kai hannu yayi zai tabata tayi saurin rintse idonta tare da girgiza masa kai, tsayawa yayi sororo yana kallonta daidai Ikcn da Mom ta gama siddabarunta ta fice.

Safnah ce ta farka ta fara mitar neman abinci ya miqe da sauri ya daukota ya kwantar da ita a gefen Habeey yace “yi hqr daughter bari na hada miki abincinki kinji" kallon Safnan ne ya rinqa mayar Mata da tunaninta baya kalamansa na batanci da tozarci gareta suna dawo Mata kazalika mgnr da taji wannan mutumin daya rungumeta dazu yana fasa cewa an daura auren Taheer da Saudat Kuma Saudat qanwarta ce.
Cikin wata murya tace “ina Addah waye ya kawoni nan kai me kakeyi anan qarfe nawa yanzu?" Cikin mamakin tambayoyin nata yace “kiyi hqr gobe zan baki amsa yanzu darene Kuma kina buqatar hutu kin kallah 2:33am fah" bata qarayi masa mgn ba har ya gama hadawa safnah madarar yazo ya dauketa ya rinqa bata tanasha tana bangale masa baki shima yanata yimata waqoqinsa itadai Habeey kallonsu kawai takeyi tana hawaye tunaninta saceta Taheer yayi ya sakeyi camping dinta a wani gurin.

A hankali tace “Taheer Ina ne nan meye ya kawoni nan Ina matarka da kazo gurina a wannen daren yaushe? Yaushene zaka gane Annabi ya faku ka qyaleni ka fita daga rayuwata ne, meye yasa kullum burinka ka quntatawa rayuwata ne Taheer kai kace na barka bakaso na bazaka iya rayuwa da karuwa ba na hqr na barka to Kai meye ya dawo dakai cikin tawa rayuwa..." Maimakon yabata amsa kawai sai taga yayi wani dogon murmushi ya daga yarsa sama ya cillata ya cafe yace “beautiful daughter ta qoshi sai bacci ki qyale Dad da Mom Suma suyi bacci ko?" Yayi mgnr yana sauke idonsa akan Habeey ya kwantar da yarinyar yace “aini mayene akanki banida zuciya Kuma bana fushi bazan taba barinki ba ke idanma tunanin na saceki kikeyi naji na amince ni barawonki ne amma wannan karon ban saceki nayi camping dinki don na aikata fasadi dake ba aa kawomin ke akayi matssyin matata ta sunnah"

Yana fadin haka ya dagota gaba dayanta ya miqar da ita tsaye qafafunta na rawa saboda rashin qarfi yaja numfashi Ikcn daya sauke idanunsa a saman boobs dinta komai ya ragu a jikinta amma banda nononta da mazaunanta.
Numfashi ya fuzgo da qarfi yanajin wani yanayi na ratsashi amma komai rashin imaninsa dole dai ya dagawa Habibatullah qafa a wannan taqin, jinginata yayi a jikinsa ya kaita bathroom ya sake mata wanka bataso amma batada ikon hanawa saboda babu kowacce gaba da take aiki yanda ya kamata a jikinta tanajin yanda yamai da hankalinsa wajen wasa da nononta yana wani shaqar numfashi yana kallon qwayar idonta.

Shassheqar kukanta yasashi saurin dakatar da abinda yakeyi ya dagata suka fito ya dauki wata rigar baccin ya sanya mata ya dauko turare zai fesa mata tayi saurin girgiza kai yayi murmushi yace “saboda kina baqin cikin kada naji qamshi naji shauqi a raina? To ai Habibatullah ko gawarki indai zaa barni naganta sai naji Ina sha'awarta saboda badagani bane abin a jininmu ne dani dake babu Wanda zai iya rayuwa babu daya"
Keda baki gurin idan kin tanka masa ta tanka tunaninta yafi karkata akan mutumin dayazo mata da baqin Ibrn an daura auren Taheer da Saudat to shidin waye da yake iqirarin shi mahaifinta ne Kuma meye alaqarsa da Saudat dama iyalan Maje Bauchi baki daya?"

Da wannan tunanin taji Taheer ya shige jikinta yana sunsunarta jikinta ya dauka rawa ya dago idanunsa da suke qara qanqancewa idan jaraba na cinsa ya saukesu a saman fuskarta da taketa malalar da hawaye.
Batayi aune ba sai kawai jin harshensa tayi saman kuncinta yana lashe hawayen nata yana qara shigewa jikinta cikin rawar muryarsa da take firgitata a baya yace “wata uku My life mijinki bai samu komai daga gareki ba don Allah kiyi playing dina na samu relief" idanunta ne suka qara kawo ruwa murya a tsittsinke tace “ba...bazan iyaba Taheer kada mu mayar da haram abincinmu don girman Allah nayiwa Addahta alqawarin bazan qara zina ba meye yasa kullum kakeson sani kaffara waccen ma daka doramin banyi ba har yanzu pls don Allah"

Hade bakinsu yayi yana “tsotsar bakinta yana goga dick dinsa a cinyarta gabadaya ya susuce yana wani nishi itakam tsoro jarabar Taheer takeyi idan abinsa ya tashi bayaji baya gani.
Daqyar da taimakon kukan da yaji tanayi har tana shidewa yasashi qyaleta amma Saida ya fitar da sperm dinsa sannan ya samu nutsuwa ya kwantar da kansa luf a jikinta yana mayar da numfashi da ko wanka bai iyayi ba bacci ya daukeshi itakam batayi bacci ba tunani yaqi barin ranta hakanan maganganunsa sukeyi Mata yawo a ranta takasa manta kalamansa mafiya muni

cikin rayuwarta “banzar ballagazar karuwar yarinyar nan" rintse idonta tayi tanason hade qarfinta ta tureshi amma babu hali batada qarfi ko na kwabo itadai ta dade da sallamashi ta hqr da rayuwa dashi koda shi kadai yayi saura namiji cikin wannan duniyar.

Kwana tayi idanunta a bude tarr Kiran asuba ne ya farkar dashi ya janye jikinsa daga nata 9 shiga bathroom yayi wanka ya dawo ya dagata cak itama yayi Mata tanajinsa harda wani sanya hannunsa yana zagare gabanta dashi tayi saurin hade qafarta tana ajiyar zuciyar takaici yace. “Ina roqon Allah ya nunamin ranar da zan sake ratsa gonata a matsayin manominta na halak malak nayi shuka nayi ban ruwa sosai ta yanda yabanya me kyau zata fito Mamana ta samu qanne ba tare da bata lkc ba, Habeeytah inasonki"
Lumshe idonta tayi ya dagota yayi Mata alwala sannan shima yayi suka fito yasa Mata doguwar rigar sallah ya jinginata jikin gadon ya rinqa taimaka Mata tayi sallah saida tayi sallama sannan shima yayi tashi yayi mata addu'a sosai sannan ya juyo ya dauki wayarsa ya kira Abba shidai Abba a tsorace ya daga wayar yace “gabana faduwa yakeyi Lele meye yake faruwa?"
